[1:51PM, 11/12/2016] +234 703 007 7024: 💞💞 *MAI SONA* 💞💞
*1*
BY *Reefat Yahya*

Bismillahi rahmanirraheem....
*note* ~is just a short n imaginary Lov story~ *hapy reading*

Zaune take tana kallon farin watan da ya haskaka ko ina...yanayin sararin samaniya take kallo yana matukar debe mata kewa ga wani iskan dake kadawa a hnkli ta lumshe ido tana jin wani nishadi amma kash!! Rashin masoyin nata kusa da ita shine babban matsalarta a wannan lokacin a hnkli ta furta "Allah sarki *mai sona* yana raye ne oho? Idan yana raye kuma nasan dole yayi auri yana can tare da matarsa ya manta dani a rayuwarsa" wani sirirn hawayene ya fito a idanunta dai dai lokacin aka dafa kafadarta ckn firgita ta juya a hnkli tsohuwar ta xauna a gefe fuskarta dauke da murmushi "jikata kiyi hakuri ki cigaba da adua wata ran Allah xai bayyana masoyin naki idan da rabon xaku sake haduwa"ta kwantar da kanta ajikin tsohuwar tana hawaye dakyar ta rarrasheta ta daina kukan da take tana bata tarihin xamaninsu haka nan ta mance da duk wani damuwar da take cki...
 Da safe ta tashi ta share gidan nasu fes tayi wanke2* bayan ta gama ta fada wanka tana fitowa a falon tsohuwar ta hadu da mahaifinta har kasa ta xauna Suka gaisa ya amsa ckn faraa da sakin fuska "er Abba yaushe zaki koma makarantar taku? "Abba IT xamuyi ba skul xamu koma bah" "toh yayi kyau Allah ya taimaka ya bada saa" "ameen nagode" daga nan tayi shigewarta daki ta shirya ckn atamfa mai kyau ta fesa turare a nan na tsaya na kare mata kallo...doguwace ba har can bah, tsayinta dai2* da jikn da take dashi wankan tarwadace tana da shape iya gwargwado ga dogon hanci se dan karamin baki , gashin idonta xara2* se kuma dimple da take dashi ga kuma wushirya masha Allah kyakkyawace ba karya ta hadu sosai.hijabi ta dora sannan ta fito har ynxu mahaifin nata yana nan hira suke da tsohuwar ta wucesu wani bangare ta shiga wata mata kyakkyawa tana rike da tea flask ta fito daga kitchen."ina kwana umma " "Ify ya kuka tashi ya kakan naki" "Ify alhmdllh" daga nan matar tayi shigewarta falo nan tabi bayanta tace "umma akwai aikin da xan tayaki dashi ne" "babu na rigada na gama" tayi shiru wata budurwace ta fito daga ckn dakin bacci hannunta dauke da cup da ruwa a cki se kuma brush da toothpaste "ina kwana anti maryam" ko uffan bata ce mata bah tayi ficewarta waje tayi brush se da ta gama ta dawo falon ta galla mata harara tace "nikam bansan ke wace irin halitta bace..a ckn gidan ma yawo xaki dinga mana da hijab, wllhi umma da islamiya kawai kuka turata Abba ya daina bata kudinsa a banxa don wannan batayi kama da en boko bah" "uhmm Abban naku shiyake biye mata ai nikam na rasa gane kan ruhaimat wllhi..kin fita daban ckn ya'yana " wacce aka kira Ruhaimat ta sunkuyar da kanta kasa tana sauraronsu idan da sabone ta saba muryar maryam naji tana cewa "in banda kauyanci ya xakima mutum magana ko brush beyi bah"😳🙊 hmmm....muryar Abba Suka ji yana cewa "sannu Ya'r birni ..wllhi maryama ki kiyayeni fah,kullum ina gaya muku Ku daina sangwamarta amma Baku jin magana , kuji tsoron Allah Ku canza hali " ya juya gun umma yace "me kuma Allah yaganar dake ..ban taba ganin wacce take sangwamar Ya'r cknta ba sai ke ,ki dai bi a hnkli ita wacce kike rainawa... "Dakata Alhaji..nifa ba tsanarta nayi bah, ina Neman wayar da kantane sabida naga tana ckn

duhu.da kke xancen na tsaneta kuma wannan kai ka janyo saboda anki a rada sunan mahaifiyata don son kai ka sanyawa taka mahaifiyar " murmushi yayi tare da cewa "Allah ya ganar dake Halima, er Abba taho muje mu ci abinci koh" sumui2* ta tashi tabi bayan mahaifin nata umma da maryam sukabi bayanta da harara.

😘😘 *Reefat CE*
[1:52PM, 11/12/2016] +234 703 007 7024: 💞💞 *MAI SONA*💞💞
*2*
BY *Reefat Yahya*

*Asalin labarin*
Alhaji Abubakar Hammawa shine asalin sunansa..su 3 iyayensu Suka haifa , Alhaji Ahamdu shine babba yana aikin gwamnati a garin kano yana da mata 2 da yara 8. Sai Hajiya maryam wacce take aure a yola ma'aikaciyar asibiti senior nurse ce *FMC*yola yaranta 4, se Alhaji Abubakar shine auta.asalinsu mutanen garin jada ne na jahar Adamawa a can aka haifesu har suka girma.mahaifinsu Allah yayi masa rasuwa se mahaifiyarsu Hajia Aishatu wacce suke kira da Hajja Dada , Alhaji Abubakar yayi karatun primary da secondary daga nan ya fada kasuwanci har Allah ya buda masa yayi aure ya auri Halimatu er garinsu.ya'ya 6 Allah ya basu Mohammed ( Hamma).. Ahmadu..Zainab..Yusuf..maryam..Aisha ( Ruhaimat) daga nan haihuwan ya tsaya musu cak..halima taso a sanyawa Ruhaimat sunan mahaifiyarta Amma Alh Abkr ya sakawa tasa mahaifiyar sunan yarinyar daga wannan lokacin umma take jin haushin surukar tata harda ita jaririyar. Mohammed wato Hamma yayi karatunsa yana aikin banki a can kano ya auri Ya'r baffansa Ahmadu, Ahmad Wanda ake kiran tijjani yayi karatunsa shima da ya kammala degree ya fada kasuwanci yana aiki tare da mahifin nasu duk fadin garin jada ansan shagunansu ya auri wata Ya'r jada suna xaune yaransu 2,se zainab wacce take yola da aure bata aikin kome mijinta barrister ne suna da yara 2,se Yusuf ya kammala karatunsa yana bautar kasa a nan garin jada Maryam wacce take aji 4 a jamiar modibbo Adama uni of tech yola.sannan auta Ruhaimat wacce take Adamawa state uni tana aji 3 a bangaren biochemistry ynxu xasu fita IT wannan kenan.

*Cigabn labari*
Bayan sun kammala kari ita da mahaifin nata ta gyara masa falon daga nan ta wuce bangaren Hajja Dada.. tana xaune a falonta "jikalle kin dawone" "nadawo takwarata" "kin ci abinci kuwa..gashi na ajiye miki , wannan Mara kunyar yayar taki ta kawo ina tambayanta kina ina bata amsa min bah" "hmm anti maryam se a hnkli" "ko ina xata samu mijin aure da wannan rashin kunyar tata oho" dariya sosai Ruhaimat take tana ckn haka wayRta ya hau ruri "masoyiyata" sunan da tagani kenan ta daga tana murmushi "Allah sarki tawan nayi missing naki" "haba ruhi Nah shine kwana 2 ko flashing babu" "yi hakuri kinsan idan ina kusa da Hajja Dada baa cewa komai" "uhmm..wato xaki manta da kowa kenan harda *mai sona*" ckn sauri tace "a'a rufamin asiri, idan na manta da *mai sona*ai ban numfashi a duniya kenan" "uhmm..ruhi kenan har ynxu de kina nan kina fama da son mutumin da baki San ko ya mutu ko yana Raye bah" "insha Allah yana nan da ransa don ina jin ajikina na kusan haduwa dashi" "toh malama Juliet Allah ya bayyana shi" "ameen nagode" haka Suka cigaba da waya daga bisani sukayi sallama.

😘😘 *Reefat ce*
[1:53PM, 11/12/2016] +234 703 007 7024: 💞💞 *MAI SONA*💞💞
*3*
BY *Reefat Yahya*

Da misalin 4:30pm wani yaro yashigo yace ana sallama da Ruhaimat maryam tayi dariya tace "jeka abunka tana nan fitowa" daga nan ta tashi ta nufi bangaren Hajja Dada Ruhaimat na kwance rike da littafin *bulagul husum* tana karantawa " malama Ruhaimat wani yana sallama dake yana jiranki" ta xare ido tace "wayene anty maryam" ta tabe baki tace "nasan miki..ko ustazunki ne yazo who knows " "nidai banyi da wani akan xaixo wajena bah" "ya rage naki yarinya..in banda wahalalle ma waxai xo wajenki xance mtsww" daga nan ta juya ta tafi Hajja Dada ta juya tana kallon Ruhaimat tace "kije mana takwara..jeki duba wanene" "gskiya babu inda xani" "bana son gardama tashi kije" ta mike se faman kumbure2* take dole ta xare hijabinta ta xumbulashi sannan tayi hanyar fita , maryama na xaune tana danna wayarta da alama chat takeyi tana ganin Ruhaimat ta xare ido tare da cewa "na shiga 3 ni Ya'r gidan siddiki hammawa..ahakN xaki fita? Kim xumbula dogon hijabi har kasa tamkar matan liman😂😂 ahakan xai soki?" Ruhaimat ta daure fuska tace "idan bai masa bah yayi gaba dama bani na kirashi bah" daga nan tasa kai tayi ficewarta.

Yana tsaye a kusa da Babur dinsa yasha gayu yyi kyau sosai wani fyn boy ne se qamshin turare ke tashi ta karasa tare da sallama ya amsa ckn jin dadi "ya kike malama " "lfy alhmdllh" "ya gida ya karatu" "lfy kalau..pls kayi sauri bana son mahaifina ya dawo ya tarar dani xaimin fada"
"Eyya sorry ..dama ba komai bane Ruhaimat na dade ina dawainiya da sonki a ckn xuciyata ..sunana Aliyu " "Aliyu nagode but kayi hakuri ina da miji" "miji kuma? ..amma seda na bincika aka tabbatarmin da cewa baki da wani tsayayye kafin naxo gidanku" "hakane Amma akwai Wanda mukayi alkawarin aure dashi kayi hakuri" "ba komai nagode Ruhaimat" nan ya cire wata katuwar Leda a bayan Babur dinsa ya mika mata taki karba nan ta masa sallama ta koma ckn gida. Yusuf yana cin abinci taxo wucewa yace "ke ..xonan" a kusa dashi ta xauna "naam yaya" "matar liman yaushe kika fara soyayya..wato an fidda tsammanin ganin *mai sona* koh" "a'a yaya..har gobe ina nan ina jiransa nasan xai zo" dariya suke harda kyakyatawa maryam tace "toh ya kukayi da wannan Wanda yazo"
"Na gaya masa ina da Wanda zan aurah" yusuf yyi murmushi yace "hmmm..inaga baki da lafiya, toh idan bahaka bah ya xaki ce kina jiran gaibu?
"Yaya ba gaibu bane *mai sona* yana..."dakata dallah, yusuf ya katseta a yayinda ya cigaba da cewa "wannan fa gaibune my dear.. For hw long zaki jira mutumin nan umm? Hw many years sukabar garinnan? Kuma idan xakiyi tunani a wancan lokacin da kuka so juna Ku yarane bakusan komai bah, ynxu ba mmki shiya manta dake Amma ke kinbi kin damu kanki kina korin maneman ki y?..gskiya ki sake tunani sis" wani yaro ya shigo rike da bakar Leda a hannunsa yace an aikesa gun Ruhaimat, maryam ta tashi ta karba tana xuba godiya ta mikawa yaron #10 sannan ya tafi ckn rawar jiki ta bude ledar turaruka masu kyau guda 3 se kuma man shafawa da chocolates a cki."wow gayen ya iya shopping wllhi daga xuwa se kaya haka..wllhi kin kofsa da mun chabe da shopping wllhi , Amma naji haushi" yusuf yana dariya yace "shegiya lashe

money" "ba zancen lashe money bah yaya..u knw irin gayu haka nake so wllhi idan xaka koma skul a maka shopping lafiyayye" Ruhaimat duk haushin yayar tata take ji daga nan ta tashi ta koma bangaren Hajja Dada.

Da dare tana kwance a bisa tabarma a waje idanunta na kallon sama ..fuskar masoyin nata kawai take tunawa ko ina yake oho! Duk inda yake ta tabbata cewa yana ckn yanayin da take a halin ynxu..tasan ya kara girma yayi kyau ga kasaita ..ta lumshe ido tare da furta "Allah sarki *mai sona* "

"aikin kenan..kowane dare a zauna ana ambaton *mai sona*..anya Ifyanki kuwa?..ni narasa gane kan wannan lamarin abin naki se gaba yake Allah de ya kyauta"

Murmushi Ruhaimat tayi tare da cewa "Hajja am ki tayani da adua Allah ya cikamin burina"

"uhmm..Allah de ya yaye miki"

Murmushi tayi ba tareda tyi magana bah.

😘😘 *Reefat CE*

[1:54PM, 11/12/2016] +234 703 007 7024: 💞💞 *MAI SONA*💞💞

*4*

BY *Reefat Yahya*

Bacci yake ckn kwanciyar hnkli bisa wani lafiyayyen gado mai kyawun gaske a hnkli take masa tafiyar tsusa agadon baya ba shiri ya bude idanunsa ahnkli yasake lumshesu ruwan sanyi ta xuba masa dan kadan a saitin fuskarsa firgigit ya tashi xaune daga shi se vest da 3qtr wando nan yabiyo ta da gudu tabar dakin Suka fara tsere ..wani tangamemen falo da xaa iya kiransa da aljannar duniya can Suka nufa wata kyakkyawar mata farasol mai masakaicin jiki tana xaune tasa TV agaba tana kallon Xee cinema award batayi aune bah taji mutum ya fada a kanta "ke Ify..". "Wayyo mami ki taimakeni bro xaimin duka" "me kike masa" dai2* nan ya karaso yana ganin mami ya shagwabe fuska yace "mami kin ganta koh...ina ckn baccina mai dadi har na fara mafarkin *mai ni*  fah taxo ta xubamin chilled water" ya karasa maganar tmkar xeyi kuka.ta juya gun yarinya ta xuba mata harara tare da cewa "tashi kiban waje Mara kunya kawai..Allah yasa ya dokemin ke tunda baki jin magana" ta tashi tsaye tana xumbura baki tace "toh mami bashi bane jiya yacemin yau xamuje national stadium kallon match din club namu..nasan baxai tashi da wuri bah shiyasa naje tashinsa" "mtsww...aikin banxa, da ruwan sanyi ake tada mutum daga bacci neh..Allah meenah ki shiga hnklinki" ta fara bubbuga kafa tace "toh ni mami me nayi" mami ta tabe baki tare da cewa "kuje can Ku gama haukar taku kunga nabiye muku har an wuceni a bada award din ma..mtsww" daga nan ta mayar da hnklinta gun kallo meenah ta juya tana kallonsa ya harde hannu a kirji yana kallonta shima " yaya am sorry" "wllhi karyanki ba u r sorry bah se na babballaki agidan nan yau" "a'a yi hakuri big bruh kar a ballamin only Dota" muryar mahaifinsu Suka jiyo yana shigowa fuskarsa dauke da murmushi meenah tana ganin haka ta ruga aguje xata fada Jikinsa ya daga hannu✋🏽"dakata madam..my wife first" nan ya sumbaci mami a goshi yace "matata hasken idaniyata far in ckn rayuwata dafatan kin tashi Ify" murmushi tasakar masa ta amsa da cewa "alhmdllh mijina uban ya'yana dafatan kaima haka" "alhmdllh shine baki tasheni bah kinsan yau ranar Ku ne bani da lokacin kowa se na iyalaina abun alfaharina" "haba baban meenah kasan bazan tasheka bah saboda nasan ka gaji sosai

yaune ranar hutunka " murmushi sukewa juna meenah tace "oh mami n Baba ikon Allah..soyayyarku bata tsufa" "my bby gal ai shi so baya tsufa saidai su masoyan su tsufa" "toh..nima Allah yabani masoyi Wanda zai soni har abada"
"Ameen dear..idan kinyi dace da masoyin kwarai kin more Rayuwa" mami CE ta fada ayinda take kallon mijin nata "morning baba" "morning son ya kake" "Ify alhmdllh" "ya naganka da vest at dis hour" "ga yarinyar nan Mara kunya ita ta katsemin bacci mai dadi wllhi" "sorry son..baby gal meyasa kikayi haka ba kyau avoid it pls" ta bata fuska tace " tashinsa kawai nayi fan..kuma yacemin da safe xamuje kallon fbal match " "duk da haka de da zaki jira ya tashi da kansa koh, is ok kuje Ku shirya kuyi wanka kuxo muyi brkfast ni yunwa nake ji" daga nan kowannensu ya wuce bangarensa don shiryawa.

Ambassador mukhtar Aliyu kenan tare da iyalansa hajiya zainab macece mai kirki da sanin darajar Dan Adam hafaffiyar garin yolace na jahar Adamawa sunyi sosai matuka tare da mijin nata tun haduwarsu a jamian mautech...tana karatu shi kuma aiki yake a makarantar a haka Suka fara soyayya har ha kaisu ga yin aure.

😘😘 *Reefat CE*
[1:55PM, 11/12/2016] +234 703 007 7024: 💞💞 *MAI SONA*💞💞
*5*
BY *Reefat Yahya*

~short n imaginary lov story~

Sadik da meenah sune yaran da Allah ya basa yadau son duniya ya dora akansu yana matukar ji dasu.sadik ya kammala karatunsa na degree a Cyprus da masters a UK dawowarsa kenan daga UK bai wuce 1 week bah a gidansu dake can birnin tarayya, meenah ko tana aji 3 a jamiar base dake garin Abuja.Ambassador mukhtar Aliyu shine ambassadan Nigeria na Amurka ya tara dukiya mai dumbin yawa saboda ya rike mukamai daban2* har xuwa lokacin da aka basa ambassador yana da kamfanin motoci a Lagos da kuma kamfanin sarrafa shinkafa a can kano sannan ya bude wani sabon kamfanin sarrafa drinks da ruwan sha ingantacce Wanda duk duniya ansan da xaman kamfanin maisuna *AMZ* a can garin yola..akwai amz water , amz orange drink, amz mango drink, pineapple drink, apple drink n guava drink.katafaren kanfani ne yayi fice sosai a kasashen duniya duk inda kaje xaka ga amz drink wannan kenan.

Suna zaune a babban teburin cin abincin se karan cokula kawai kake ji kas..kas sunyi shiru suna cin abinci dama al'adarsu kenan idan suna cin abinci babu mai magana a cknsu har sai sun gama.bayan wani kankanin lokaci sun kammala cin abincin ambassador mukhtar ne ya fara magana " dana kayi karatu ka gama Allah ya albarkaci abunda ka karanta" gaba daya Suka amsa da ameen" ya cigaba da cewa "naso a ce kayi aure kafin ka fara aiki Amma tunda Allah baiyi bah..ka cigaba da adua Allah ya fito maka da mace ta gari , ynxu ka fara shirye2* next week xaka koma can yola ka kula da amz company" ya daga kai ckn tsananin jin dadin an ambaci sunan yola yayi saurin cewa "ba komai baba insha Allah I will make u proud" "haka nake son ji..ka tsaya ka kula da aikinka kuma kada kayi wasa da ibadanka" "insha Allah zan kiyaye" "Allah ya bada saa" "ameen" ya juya gun matarsa yana murmushi yace "kinyi shiru..baki ji dadin hukuncina ba  koh, kinfi son danki ya xauna kusa dake ki shagwaba shi" "ba xancen

shagwaba ba Alhaji..idan yaje yola wa xai kula dashi" "don't wory shi ba karamin yaro bane xai kula da kansa kedai ki tayashi da adua ok" a hnkli ta furta "ok Allah yasa hakan shine mafi alheri" "ameen" meenah dai ko uffan bata CE bah ta cigaba da kurba tea tana binsu da idanu bayan ta gama ta ajiye cup da karfi Suka juya suna kallonta tace "kuna zancen wazai kula dashi bayN kunsan cewa *mai ni* tana can yola tana jiran xuwansa, Baku lura da yanayin da yake cki bah..se murmushn jin dadi yake tundazu ina observing" "ke ..bana son iskanci fah, da nasan gidansu *mai ni* zan tsaya bata lokaci a nan garin ne? But anyway Allah ya cikamin burina ya bani ikon ganinta ckn sauki" baba ya juya yana kallonsu yace "kun tsakamu a duhu..wacece kuma *mai ni*??" "A'a sundai saka ka a duhu..inda sabo ai na saba da jin wannan sunan , waka ce kawai ya rage " "bangane me kke nufi bah" "uhmm..gasu nan ai ka tambayesu" ya juya gun sadik yace " wacece mai ni????

🤔🤔🤔wacece???
[1:55PM, 11/12/2016] +234 703 007 7024: 💞💞 *MAI SONA*💞💞
*6*
BY *Reefat yahya*

~a short n imaginary Lov story~

"Baba ka tambayi yaya..shine yake bamu labarinta kullum se yayi mafarki da ita" "mafarki kuma?..ko mafarkin jinnul ashiq yake" da sauri ya daga kansa yace "c'mon baba she is a human being pls" "am not sure she is" mami ta fada ayayin da ta mike tana shirin barin teburin cin abincin "mami trust me Allah " "zancen banxa" daga nan ta koma falo baban nasu yace "den tell me ya akayi kuka hadu ..a ina ka taba ganinta kuma ina take xama " "baba gskiya bansan ina take bah a halin da ake ciki don na dade ina nemanta bansamu ganinta bah" "ok wane gari take" "9yrs back lokacin da mukaje yola Hutu na raka uncle Suleiman ( kanin mami ) garin jada , lokacin yana bautar kasa a can garin ..na hadu da ita a GSS jada tana jss1 mun shaku da juna sosai har nayi mata alkawarin aure" me meenah xatayi inba dariya bah tace "God...I can't bliv dis, yaya daman duk wannan haukar akan er jss1 kake?..hhhh" "quite pls..meyasa baki da nitsuwane meenah 9yrs back xuwa ynxu wat do u tink? ..maybe ta gama jamia ma ke kina nan kina haukarki mtsww..continue son ina jinka" sadik Wanda ransa ya gama baci ya kalli baba yace "kana gani koh baba..Allah meenah ta raina ni but xanyi maganinki , ba don ina sake miki bah..gud zan dau mataki akai" "sory yaya wllhi ni I tot a Cyprus kuka hadu da ita kuma kace min er yola CE daz y abun..."
"Rufemin baki...ki barnan ynxu b4 d count of 3" ganin babu alamar wasa a fuskarsa ne yasa ta tashi ta koma falo kusa da mami ta xauna se wani kumbure2* take.sadik ya cigaba da cewa "nayi 2months tare da ita mun shaku sosai..lokacin da na koma yola after 3 yrs naje nemanta aka ce tabar makarantar , na nemi gidansu na rasa saboda bata taba nunamin gidan bah kullum a skul muke haduwa n bansan kawaye ko en uwanta bah..ita kadai nasani" ya ja dogon numfashi tare da share hawayen fuskarsa baba yayi shiru yana kallon dan nasa gskiya ya tausaya mai kuma tabbas yana kaunar yarinyar ba wasa..haka ya bashi baki akan yayi hkri in Allah ya yarda wata ran xasu hadu kuma ze tayashi da adua a haka Suka rabu.

***************

Ruhaimat ce xaune a falon Abba yana shan tea yace "toh mama na Allah ubangiji ya baki saa kiyi karatu sosai banda wasa kinji" "nagode Abba" "Allah  ya miki albarka" "ameen" umma ta shugo tana murmushi "maman Abbanta xaki tafi kenan" "ehh umma xan tafi" "Allah y kiyaye hanya idan kinje ki gaishemin da xee Tah" "xataji insha Allah" Abba ya fito da kudi ya kirga 30k yace "mamana ga wannan ki rike se munyi waya koh" "Abba nagode Allah ya kara budi" umma ta tabe baki tare da cewa "su er gata bah" basu tanka mata bah Ruhaimat ta tashi ta musu sallama ta koma bangaren Hajja Dada ta shigo da sallama anty maryam ce kwance a bisa kujerar xaman mutum 3 tana chat se murmusawa take , Ruhaimat ta fito da jakar kayNta "Hajja tah na tafi ..anty maryam na tafi se munyi waya" "er Albarka Allah ubangiji ya baki saa ya tsare min ke" "ameen kakata Allah yabar min ke" maryam ta juya tana kallonta tace "ikon God!yarinya tafiyar ma se da hijabi, wllhi mijinki ya shiga 3 " Hajja dad tayi carab tace "hijabi su2race kuma Allah zai bata miji nagari nitsasse me hali irin nata" "yoo kice min ustazu mana mai dangalelen wando mai hana kudin anko da fita gidan buki ko suna, idan ba ustazu bah ai mazan ynxu basa son mace mai yawan saka hijabi..ganin karuwa ko mai boye ckn shege zasu miki gara ma ki daina" salallami Hajja Dada take tana mamakin kalaman maryam Ruhaimat kam ko ajikinta murmushi kawai take daga nan ta daga jakar tayi waje Hajja Dada ta rakata har kofar gida wani idi dan unguwar shiya rike mata jakar xuwa bakin hanya , tana nan tsaye bayan minti 15 ta sami mota nan ta biya kudin 600 Suka dau hanyar yola.

*Reefat CE*😘😘😘
[1:56PM, 11/12/2016] +234 703 007 7024: 💞💞 *MAI SONA*💞💞
*7*
BY *Reefat yahya*

Tafiyar 2hrs kacal sukayi daga jada xuwa yola a bakin kasuwa ta sauka ta nemi abun hawa daga nan ta wuce gidan anty zainab yayarta matar barrister. ta shigo tare da sallama tana kwance a kasan kafet kallon film take ckn murna Suka rungumi juna dama can tafi shiri da anty zee akan anty maryam , ta kawo mata ruwa mai sanyi tasha nan Suka fara hiran yaushe gamo tana tmbyrta labarin gida haka Suka kasance har xuwa lokacin da mijinta ya dawo tare da yaransu ya daukosu daga makaranta.

Washegari...Ruhaimat tayi kwalliya ckn wasu lace milk n purple ta saka purple hijab dama can ba gwanar make up bace hoda da lipgoss kawai ta saka tayi kyau ga qamshin turarenta mai sanyi tayi sallama da anty Xee daga nan ta wuce gidan babbar aminiyarta sadiya Ahmad wacce take kira da masoyiyata ,bata da abokiya da ta wuce  sadiya kullum suna tare a can state uni hostel daya komi nasu daya Amma banda hali cos sadiya tana da shegen suru2 gata da son kwalliya kuma a duniya babu abunda ta tsana irin hijab wannan kenan.

Ta shigo gidan tare da sallama sadiya ta fito Suka rungumi juna suna dariya "idonki kenan ruhi Nah..hmm lallai yau na tashi da saa kuwa" "Allah koh masoyiyata" "ehh..mana er Abba da kanta har gidan mu am so lucky gskiy" "banson iskanci fah" "yi hakuri toh mu shiga cki" dakin baccinsu Suka shigo bayan ta gaisa da Mmn sadiya. "So yaushe zaki fara xuwan training " "ni..gobe nake son farawa kinsan next week supervisor zai zo" "hmm ba gara ke bah, Allah ya hadaki da mai dan saukin kai..nikam wannan shegen mr bulus yakubun se wani girman kan

tsiya ga muni mtsww" dariya sosai Ruhaimat take harda rike cki "Allah kina ban dariya sadee...meyasa baki roki HoD ya canza miki bah" "hmm kina magana tamkar baki San halin mutanen dprtmnt bah..gasu nan munana amma se girman kan tsiya" "Allah ya bamu saa yasa mu rabu dasu Ify"
"Ameen" har yamma Ruhaimat tana gidan su sadee dakyar Suka rabu ta koma gida.
Da dare suna xaune a falo suna kallo wayarta ya hau ruri Hajja Dada CE nan ta daga sun dade suna hira tana jin muryar anty maryam tana tsokanar Hajja ta mikawa anty zee sun gaisa daga na ta karbi wayar sun Dade sosai suna hira daga karshe sukayi sallama tana ajiye wayar wani call ya sake shiga new num ne tayi picking tare da sallama "ya kke malama Ruhaimat ya hanya dafatan Ify" "Ify alhmdllh but sorry bangane mai magana bah" "kina magana ne da masoyinki" tayi shiru ta rasa me zata fada "kiyi hakuri na karbi layinki widout ur permission" "ba komai but kayi hakuri inada Wanda zan aura" "Ruhaimat kina maganane da Aliyu daga jada" "oh Aliyu dama Kaine?.."ehh wllhi jiya nahadu da anty Maryam ita taban layin" "ok nagode da kira sai da safe" "haba Ruhaimat ki saurareni pls..nasan kin gayamin kina da Wanda zaki aura , but tunda bai kawo sadaki ba it doesn't matter " tayi saurin taresa "no it matters Aliyu baxan iya cin amanar masoyina ba pls gud nyt" diff ta kashe wayar anty Xee ta juya tana kallonta ckn mamaki ta tabe baki tare da cewa "wato har ynxu kina nan kina fama da haukan aljanin nan naki *mai sona* ne ko mai menene, anya Ruhaimat Ifynki kuwa?..gskiya xanyi magana da Abba ya nema mki magani inaga sammu ne Suka fake a jikin ki" dariya tayi "haba anty Xee wani irin sammu kuma..wllhi *mai sona* mutum ne ba aljani bah , yana nan tafe insha Allah" "uhmm..Allah ya kyauta" Ruhaimat ta cire wayRta ta kira layin anty maryam bugu 2 ta daga "matar ustazai ya ake cki" "haba anty maryam ya zaki bada layina gun mutumin da baki sani bah..kuma na gayamiki bana sonsa kin..".  "Ke dallah malama rufemin baki, ni saarki CE zaki kirani kinamin fada?...wawiyar yarinya kawai, laifine don mutum ya nuna yana sonki" "kiyi hkri anty maryam Amma don Allah ni bana son kina ba mutane num anyhw" "mtsww...bani da lokacin ki" daga nan maryam ta katse kiran Ruhaimat ta tashi tamkar  xatayi kuka ta koma daki anty Xee de se kallonta take tana jinjina lamarin.

*Reefat CE*😘😘
[1:56PM, 11/12/2016] +234 703 007 7024: 💞💞 *MAI SONA*💞💞
*8*
BY *Reefat yahya*

~a short n imaginary Lov story~

Da safe Ruhaimat ta gama shiryawa ckn doguwar Riga da wando pink color da touches of black ta saka bakin hijabi tare da bakin takalmi da jaka tayi simple makeup nata as usual ta fesa turare sannan ta fito anty Xee tana mopping din falon tace "iyye er Abba en mata ansha kyau" murmushi tayi "nagode anty ni xan wuce" "ki kula da kanki sosai banda shige2* duk da nasan halinki baki da rawar kai Amma de ki kula saboda amz ba wurin wasa bane ki kame kanki sosai, na taba xuwa tare da abban siyama wurin masu kudine babu maikula harkar wani Amma akwai en rainin wayo " "babu Matsala anty insha Allah abunda ya kaini kawai xanyi" "toh Allah ya taimaka ya bada saa" "ameen tank u" daga nan tasa kai tayi ficewarta keke napep ta shiga

direct basu tsaya koina bah sai *Amz* company , bayan ta biya kudin ta shiga tun a bakin gate xaka gane lallai ba karamin company bane securities suna tsaye se ka nuna Id card kafin ka wuce idan ka wucesu kuma security doors ne ta nan xakabi ka shiga harabar kamfani wani katafaren story building ne xaikai hawa 30 , building ne mai kyawun gaske idan nace zan kwatantashi ma bata lokacine.Ruhaimat ta tsaya kyamm...tarasa mexata yi kowa na harkar gabansa babu mai kula wani ga mutane birjik wasu suna shiga wasu suna fita , ga nan motoci birjik suna fitar da drinks.Ruhaimat tana tsaye wani security yaxo wucewa tayi saurin xuwa wajensa tace "pls malam tambaya nake" wani kallon sama da kasa ya mata sannan yasa kai yayi gaba ta tabe baki tace "duniya ina xaki damu..idan an ganka da hijabi de ana ganinka illiterate Mara gata hmm Allah ya kyauta" ta cigaba da tsayuwa kamar a mafarki taji ankira sunanta wani Dan dprtmnt dinsu ne ,wani farin cki ya lullubeta ya karasa Suka gaisa ya shaida mata cewa a nan yake IT ta rokesa ya nuna mata inda ake reporting daga nan tabi bayansa elevator Suka shiga.

Wani dankareren office ne wani mutum ya hakikance a bisa office chair se juyawa yake "excuse" ya share minti 5 kan ya amsa musu da "com in" kallo daya yamusu ya dauke kai, Ruhaimat tayi masa bayanin komai yana kallonta da mmki don batayi kama da wacce ta iya turanci haka bah..ganin er kauye illiterate yake mata.wasu takardu tayi signing ta cike komai ya gaya mata offishin da xataje tayi reporting godiya ta masa Sukayi ficewarsu. Bayan ta gama duk abunda ya dace tayi nan Suka shiga ana musu practical yanda xasu gudanar da komai an musu bayani tana rubutawa, lokacin sallan azahar yayi kowa ya fita Ruhaimat ta juya kenan Suka hada ido da wata er budurwa murmushi Suka sakarwa juna "sannu koh..sunana Ameena" "sunana Ruhaimat" "nice meeting u" "u too..Amma yau kika fara xuwa koh" "ehh wllhi yau nayi reporting" "ok muje muyi sallah akwai masallaci a can kasa" daga nan Suka fita suna hira.

*Reefat CE*
[1:57PM, 11/12/2016] +234 703 007 7024: 💞💞 *MAI SONA*💞💞
*9*
BY *Reefat yahya*

~short n imaginary Lov story~

Zaune yake a katafaren falonsa yayi jugum yana tunani meenah ta shigo kusa dashi ta xauna ko kllon bangaren da take baiyi bah "yaya am sorry kayi hkri Allah wasa nake mah..am sorry pls" "tashi ki bar nan bana son ganinki" "eyya pls.." "I said leave n I min it" ya fada ckn tsawa nan ta tashi har ta kai bakin kofa ta sake dawowa " yaya shawara xan baka..y not kayi searching sunan *mai ni* a fbuk ko xakayi dace" ya kura mata ido tamkar mai naxarin wani Abu ya tashi tsaye yace "yess...gud girl u r right" phn nasa ya dauka daga ckn daki ya dawo ya xauna meenah tana murmushi ta maso kusa dashi ta xauna. Fbuk ya bude yayi searching Ruhaimat Abubakar no match found haushi kamar xe mutu take ya wurgar da phn din meenah tayi saurin cafke shi if nt da babu abunda xai hana screen fashewa tace "calm down pls..am sure she is on fbuk just tink of anoda name" "hakane fah..bani wayar na tuna real name nata Aisha" nan yayi searching Aisha Abubakar ga sunaye birjik meenah tayi saurin karban phn din "nasanka da rashin hakuri kawo ni xan duba" tana shiga profiles dinsu daya bayan daya Aisha

Abubakar username Ruhaimat hometown jada state Adamawa student of Adamawa state uni "yaya kaga wata mai...bata karasa maganar ba ya karbe phn "Allah itace she is d1 " "yaya hw com's kasan cewa she is d1" ba tare da bata lokaci bah ya tura fren rqst last seen nata 3monts ago, yaja tsaki ya ajiye wayar gashi babu pix ko 1 a profile nata meenah ce ta cigaba da kwantar masa da hnkli.

************

"Ruhaimat kina yin fbuk kuwa? "Yh ..but bana yawan chatin gskiya ynxu haka namanta wen last na shiga" "watsap ko instgram ko twitter wanne kika fi so " "uhm nifa social lyf bai dameni bah ina de yin watsap somtyms shima ba kullum bah, twitter kuma bana yi gara instagram ina da acct" "ai naga alama ke ustaxiyace sosai"
"Allah bahaka bane ..just am too busy bani da lokacinsu ne" "nidai ki shiga ynxu xanyi adding naki Ruhaimat waye? "Aisha Abubakar ( Ruhaimat) " "ok" Ameena ta bude data ta shiga fbuk " gashinan na gani babu pix a profile ko" "ehh..shine" Ruhaimat ta shiga duba mssgs da kuma notification friends reqst sunkai 40 deletin kawai take taxo kan wani suna tayi shiru tare da kurawa wayar ido "laa..kinga wani mai sunan Abba Nah,kuma sunan nasa sounds familiar.. Anyway lemmi just accept him ko don sunansa" tayi accptin he is active kuma , tayi accptin din Ameena suna ckn hiransu Abubakar mukhtar ya tura mata mssgs "salam dia fren tnx 4accptin me" "uw" "ya kke " "Ify n u" "same..pls idan baxaki damu bah tmbaya xan miki pls" "ok go on" "Ke er jada CE" "yh "
"I donno but by any chance kin taba soyayya da wani 9yrs back..."😳😳😳😳
" *mai sona*! "Waat... *mai ni*ya Allah I can't bliv dis "
"Mai sona ..dama da rabon xamu sake haduwa" "Allah sarki maini I rily rily miss u ..I miss darm much" "I miss u more..mai sona yaushe xan ganka ur Lov almost killed me" " main hoona ( am here now) worry not my Dil I'll b on my way very soon insha Allah" "can't wait to c u kismat Nah" "me too" Ameena tace "Ify kuwa se murmushi kike ..da waye ake chatin haka? Kodai mr right ne" Ruhaimat ta fada jikin Ameena tana dariya "kawata am I dreaming.. I rily can't bliv dis nayi chat da *mai sona* " "waye shi? "My kismat" Ameena ta tabe baki tace "ikon Allah wannan wane irin so kike masa kuma menene kismat???

*Reefat CE*😘😘
[1:57PM, 11/12/2016] +234 703 007 7024: 💞💞 *MAI SONA*💞💞
*10*
BY *Reefat yahya*

~short n imaginary Lov story~

Yinin ranar Ruhaimat tayishi ne ckn walwala da farin cki baki har kunne tamkar wacce ta samu kujeran hajji ko kuma Wanda akayiwa albishir da gidan aljanna.ta xayyanawa anty Xee halinda take cki ta tayata murna sosai da dare ta sake shigan fbuk yana mata korafin ta tafi ta barshi da kewarta yace ta tura masa num xe kirata babu bata lokaci ta tura dama kwance take a daki ita kadai se faman lumshe ido take karar wayarta ne katse mata tunanin da take "salamu alaikum" "mai ni...muryarki kenan ko mafarki nake " "mai sona"..se kuma ta fara kuka a hnkli "maini kina

jina..shiru bata amsa bah "helo kina jina pls talk to me"  a hnkli ta furta "ina jinka" haba maini duk kinbi kin dagamin hankali" "am sorry kukan farin cki nake "

"No..pls Dil bana son wannan kukan stop it " "ok. I'll" "yawwa smile ...tamkar yana ganinta tayi wani lallausan murmushi tana lumshe idanu wani shaukin sonsa take ji "maini baki daina kukan ba ko" na daina fah" "toh meyasa baki min magana " ina sonka sosai" murmushi yayi daga bangarensa yace "nima haka..so hw lyf hw have u bin" "alhmdllh.. Ya bayan rabuwa" "Ify kalau se bakin ckn rashinki kusa I rily missed u Ruhaimat" "I missed u more so ya skul am sure ka gama" "yh har nayi masters dama jan cigaba da PhD amma sonki ya hana xuciyata sakat dole na dawo na nemeki muyi aure kafin na cigaba da karatun" murmushi tayi tare da rufe fuska tamkar yana kallonta "sarkin kunya har ynxu de baki canza bah my Dil" um um kismat bana son Neman magana" "daz d fact..anyway naga kina  state uni koh, wane course? Biochemistry ynxu na fara IT" "wow daz grt saura 1yr ki gama kenan.. But gskiya 1 yr yayi yawa I can't wait" haka de Suka cigaba da hirarsu irin ta masoya kamar xasu hadiye juna.ni Reefat nace ohh masoya kenan"

****

Washe garin Ruhaimat ta tashi ckn walwala da nishadi Wanda rabon ta kasance haka tun bayan rabuwarsu anty Xee na faman tsokanarta bayN ta kammala duk ayyukan gida ta fada wanka ta fito taci abinci sama2* sannan tayi sallama ta tafi.kamar kullum tana ckn hijabinta mai hannu tayi kyau sosai a bakin gate Suka hadu da Ameena wacce ta dade da xuwa tana jiran karasowar kawar tata , murmushi Suka sakar wa juna "ina kwana" "Ify ya gida ya *mai sona* " aa *mai sona* de ba maisonki bah" dariya Ameena tayi tace "sorry toh..ya mai sonki dafatan yana Ify" Ify kalau yau da muryarsa nayi brkfast" abun ba sauki Allah yabarku tare" "ameen kawata nagode da wannan aduar taki " daga nan Suka karasa cki direct office nasu Suka wuce ma'aikatan sunata harkokinsu dakin chemicals da ake amfani dasu wajen sarrafa drinks Suka shiga ana musu bayani dalla2* Ruhaimat tana jotting bude kofar da akayi wata er budurwa ta shigo er gayuce sosai sautin takalmintane ya janyo hankulan jama'a ji kake kwas..kwas ckn girmamawa Suka fara gabatar da gaisuwa bata amsa bah se yatsina fuska take tana binsu da kallon 3kwabo ga cingam abakinta tana taunawa  qamshin turarenta ya gauraye dakin Ruhaimat ta bude baki tana kallonta wata shaidaniyar gown CE a jikinta pitch color yayi masifan kama jikinta duk sururin jikinta a bayyane har shatin inner wears nata Ruhaimat ta cigaba da kallonta ckn rashin SAA idanunta Suka fada ckn nata aikuwa kamar jira take tayo kanta da niyyar marinta Amma tana xuwa har ta daga hnnu se kuma ta kasa wani kwarjini ne tagani a fuskar yarinyar alamarin da ya ba aikatan mamaki kenan saboda sanin halayenta kowa na shakkarta a duk fadin kamfanin "ke malama daga ina kike kin wani kuramin ido kamar tsohuwar mayya" "kiyi hakuri ni IT student ce"  "maganar banxa..mr Ibrahim ya cika kwashe2*n banxa if not ya xaayi ya kawo mana irin wannan abun a ckn company" ta karasa maganar tana bin Ruhaimat da kallon rashin mutunci ta cigaba da cewa "anyway..is very unfortunate kika zo it a wannan company, but kisani cewa munada dresscode saboda da haka ki kiyaye gaba..Jacob! "Yes ma'am" "pls tell her about our company n he we do things here" daga nan tasa kai tayi ficewarta.Wanda aka kira da suna Jacob ya juya gun Ruhaimat yace " u r d luckiest girl on earth.. Madam ta daga hannu xata mareki ta fasa, abun mamaki..sunanta hajiya yasmeen tayi karatu a kasar waje she is 26yrs old , mahaifinta hamshakin maikudi ne itace assistant manager na wannan company kowa na shakkarta batada kunya bare tausayi saboda haka Ku kiyaye "

daliban gaba daya suna mamakin halaye irin na yasmeen. Ruhaimat taja tsaki tare da cewa "aikin banxa..kara2 a kasar waje hauka ne? Ko ita ta fara xuwa ko akanta xaa daina, kowa de xai mutu yabar wannan duniya Allah de yaganar damu gskiya" Ameena ta amsa da ameen" sannan Suka cigaba da daukan darasi.

*Reefat CE*😘😘
[1:57PM, 11/12/2016] +234 703 007 7024: 💞💞 *MAI SONA*💞💞
*11*
BY *Reefat yahya*

~short n imaginary Lov story~

Ta koma gida dakinta ta nufa ta fada saman gado gskiya ta gaji sosai dakyar ta tashi ta watsa ruwa tunda ta riga tayi sallan laasar kafin ta dawo..wayarta ya fara vibrating new number ne ta daga tare da sallama ya amsa nan da nan ta gane mai magana wato Aliyu ne "ya kke malama " Ify alhmdllh ya gida ya hidima " "Ify kalau..Ruhaimat ki gafarceni xuciyata ce ta kasa samun sakat! Ina sonki wllhi ba da yaudara naxo miki bah Ruhaimat I do Lov u a lot" haba Aliyu yaxamu tsaya muna Abu kamar kananan yara..I told u dat ina tare da wani Wanda can aura shin meyasa baxaka hakura bah" am sorry balaifina bane Allah ina sonki Ruhaimat" "nagode but pls Aliyu let's stop dis" yayi shiru ya rasa me xai gaya mata kawai ta katse kiran se kuma ganin misscals din sadik har 2 nan batare da bata lokaci ba tayi dialling num yayi ringing baa daga bah, ta sake kira har ya tsinke be daga bah.. Hnklinta ya tashi tasani sarai yana da kishin tsiya. Call nasa ne ya shigo ta daga "mai sona" da waye kike waya tun dazu call waiting" em sorry kismat, wllhi wani Dan jada ne wai yana sona ni..."dakata Dil! Justsay saurayinki ne simple" haba kismat kasan babu Wanda nake so a duk fadin duniya irinka Amma tunda Baka yard dani bah fyn" duff..ta kashe wayar tana dariya tasan idan Bahaka tayi bah maganar baxai kare bah.ya sake kira har a karo na 3 ta daga nan ta fashe masa da kukan shagwaba😳😜😜 Gaba daya ta rikitashi da kukan nata..lyk serious lol ckn sanyin murya yace "my Dil am sorry pls..kinsan ina sonki sosai, bana son ganin wani kusa dake pls kiyi hakura nasan baxaki taba cin amanata bah I trust u pls stp crying" ta Dan sagaita kuka ckn murya can kasa2* tace "is ok tunda baka yarda dani bah.." "Haba I said sorry fah.. I trust u n I Lov u" murmushi tayi "I Lov u too" "daz my Dil"..muah" ta rufe fuska ckn jin kunya tamkar yana wajen "sarkin kunya! Ki ban labarin IT toh" notin special fah..so boring kawai" "eyya sory ,idan nazo I'll kip u company" "Oh tanx dia" haka Suka cigaba da hiransu Ruhaimat se juye2* take akan gado tana faman lumshe ido...oh oh! Soyayya dadi😍😍.

Yauma kamar jiya a bakin gate Ameena ta jirata tare Suka karasa an fara daukan darasi bayan sun gama masu Neman Karin bayani na gabatar da tambayoyin su a haka supervisor yaxo duba dalibansa tare da daukan attendance daga bisani ya gama aikinsa ya tafi.Ruhaimat na fitowa daga dakin koyarwa tayi tuntube da mutum garam Suka bugi juna tayi saurin komawa da baya saukan mari taji a saitin kumatun ta wani saurayine Dan kyakkyawa dashi ya harareta a yayina yake gyaran suit dinsa "next tym ki bude idanunki ki kalli hanya ..idiot mtsw" ya juya xai tafi Ruhaimat tayi carab tace "Allah ya isa azzalumi kawai" ya juya aguje tabar wajen Ameena

na dariya tabi bayanta yaja tsaki yayi tafiyarsa.

Ruhaimat ta sauke numfashi tare da Jan tsaki" mtsw..Allah wadai ace kowa in ya ganka da hijabi de se ya raina maka wayau, Allah de ya shirya" Ameena ce ta karasa kusa da ita "kawata kinsan mutumin nan kuwa? Niban sanshi bah yau na fara haduwa dashi" hmm shine sales director fah na wannan company ana ji dashi sosai, baki ga yanda en mata ke rububinsa bah" mtsww..toh ni ina ruwana idan shine manager ma I don't kia" uhmm mutanen se a slow" .sallah sukayi sannan Ruhaimat ta fara rubuta report sunayi suna hira mr Ibrahim ne ya kirasu yace su samesa a office, bayan sun gama abunda xasuyi office nasa Suka bude tare da sallama yana yan rubuce2* ga kuma wannan saurayin da sukayi karo da Ruhaimat a gefe yana danne2* a waya , zama sukayi bisa kujeru murmushi ya sakar musu "yawwa tanx 4comin..dama aiki nake son Ku tayani pls idan baxan takuraku bah" ba damuwa zamuyi" Ruhaimat ce ta amsa masa aikuwa wannan saurayin yana jin muryarta yayi saurin daga kansa ya nunata "you...me kikeyi a nan" hararinsa take...

*Reefat cE* 😘
[1:57PM, 11/12/2016] +234 703 007 7024: 💞💞 *MAI SONA*💞💞
*12*
BY *Reefat yahya*

~short n imaginary lov story~

Ruhaimat ta cigaba da hararinsa daga bisani tace "kai xan tambaya" ya tashi ya nufi inda take xaune ckn sauri ta tashi ta koma bayan mr Ibrahim ta tsaya tana mai xare ido Ameena da mr Ibrahim sun xama en kallo " director dama kasanta ne " "ehh nasanta she is my cousin" "wow..rily! Shine bakayi introducing dinta a wajena bah" mtsww..kaga ib bana son iskanci pls, nifa bansan wannan er kauyen bah kuma kai xan tamabaya a ina kuka jajibota" Ruhaimat ta murguda masa baki nan ya tunxura ji yake tamkar ya shaketa gaba daya haushinta yake ji ba shiri ya fita yabar offishin.mr Ibrahim ya juya gun Ruhaimat yace "dagaske imran cousin bro naki ne" "Allah ya tsare gatari da sarin dutse..tirr! Babu abunda ya hadani dashi" mr Ibrahim ya tabe baki tare da jinjina lamarin "lallai idan har yau kuka fara sanin juna toh gskiya abun da mamaki bcos imran baya shiga harkan kowa , kuma duk fadin kamfanin nan ana matukar shakkarsa har yasmeen tsoronsa take ji don baya sake mata" Ruhaimat ta tabe baki tare da cewa"toh ni ina ruwana dashi" daga nan mr Ibrahim ya mika musu wasu takardu yace suyi typing nan ya tura laptop agaban Ruhaimat yace "its urgent ..pls Ku tayani" babu gardama ta fara typing Ameena ta dawo kusa da ita ta xauna, misalin karfe 5 suna tsaye a bakin titi suna jiran abin hawa wani range rover mai kyawun gaske yayi parking dab dasu a hnkli aka sauke glass mr Ibrahim ne a barin driver imran kuma a gefe ya hada rai se danne2* yakeyi a wayarsa "kanwata kuzo na saukeku a gida " wani mugun kallo imran ya watsa masa yace " a wane motar, badai wannan ba koh" sorry pls..haba aboki let's drop dem" no..baxan shiga mota 1 da wannan er kauyen, gara ma kawar tata xata iya shiga" mtsww..kanka ake ji dama wayAke marmarin shiga motar ka, yaya na ba damuwa xamu shiga keke tnx" Ruhaimat tana gama fadin haka taja hannun Ameena sukayi gaba murmushi kawai Ibrahim yayi haka nan yaji yarinyar tana burgesa yana juyawa Suka hada ido da imran yace "hnklinka ya kwanta ai ..dama so kake

ka cimin mutunci" haba imran kayi hakuri mana " dallah malam ka ja mota  mu tafi..mtsw er matsiyata sai ta raina kanta wllhi" Ibrahim yana son yin dariya Amma ba hali haka ya tada mota Suka dau hanyar gida, dayake su neighbors ne kullum tare suke xuwa su koma.
   Imran Sultan modibbo only son  agidan Alhaji sultan modibbo jikan lamidon Adamawa ne su 5 gun iyayensu Amma shi kadaine namiji yana da yayu mata 2 sunyi aure se kuma kanne 2 daya tana ajin karshe a jamia daya tana aji 3. Imran dangatan gaske ne duk familyn modibbo ana ji dashi kyakkyawane ajin farko en mata har fada sukeyi a kansa shiko bashi da lokacinsu hasalima bai taba yin soyayya ba tunda yake a rayuwarsa, Ibrahim abokinsa ne Dan makwaftan su Alhaji sultan ne ya dauki nauyin karatun Ibrahim tun yana primary saboda mahaifinsa talakane mai rufin asiri..wannan kenan.
    Ko gyara parking bai gama bah imran ya Tura murfin motar ya bude fuu...yayi ckn gida a falo ya hadu da kannensa suna masa sannu da dawowa hannu ya daga musu ya haura xuwa bangarensa Momi tana xaune tana mamakin halin da taga Dan nata a cki, Ibrahim ne ya shigo da sallama " baba na yau kuma wa ya taba abokin naka" hmm..kedai bari kawai Momi, yayi sabuwar budurwa ne " wow..da gaske ya Ibrahim" Momi ta harareta tace "toh uwar axarbabi " dariya Ibrahim yake "Ummi uwar jin gulma , kije gun yayan naki ya fada miki banda ni" "kyaleta jeka ka ci abinci ka huta" murmushi yake ya nufi bangaren cin abinci.
Momi ta tura kofar dakinsa a hnkli yana nan kwance bisa 3seater idanunsa na kallon ceiling se faman Jan tsaki yake " imran meyake damunka..wani ne ya bata maka rai? Allah Momi yarinyar ta raina ni Amma xanyi maganin ta" Momi ta danne dariyar dake Neman kubce mata " wace yarinyace haka"  "wata er talakawa ce " Momi ta hada rai tace "wato har ynxu kana nan da wannan halin naka na wulakanta na kasa da kai koh..eyee imran " ya tura baki ckn shagwaba yace " Allah Momi ni bana wulakanta mutane yarinyar CE ta..✋🏽 ya isheni..tunda baka jin magana kaje ka cigaba da duk abunda kaga daman yi" daga nan Momi tayi ficewarta ya rike kai yace "ohhh..wannan yarinyar she is a dvil I wanna kill her" daga nan ya tashi yabi bayan Momi da niyyar bata hakuri.

********** Ruhaimat tana chat da masoyin nata yace ta tura masa pix nata taki amincewa wai lallai shi xai fara tura nasa, babu gardama ya tura pix 3 masu kyau😳😳 saura kadan numfashnta ya dauke..he luk so...😘😘😘 a ckn xuciyarta tace " ohh akwai kyawawa a duniya..dazu ina yaba kyawun director ashe *mai sona* ya fisa kyau masha Allah ta kurawa hoton ido babu ko keftawa.

*Reefat CE*😘😘😘
[1:58PM, 11/12/2016] +234 703 007 7024: 💞💞 *MAI SONA*💞💞
*13*
BY *Reefat yahya*

~..short n imaginary lov story~

Ruhaimat ce tsaye a bakin gate din amz da misalin karfe 10am se duba agogo take me yahana Ameena xuwa har ynxu ..gashi num wayarta baya shiga, ta kara 15mins sannan ta shiga harabar kamfanin as usual ana nuna musu chemicals daban2* bayan sun kammala aka bata

aikin da xatayi tana yi ne kawai amma hnklinta a rarrabe yake tana tunanin meyasa layin Ameena baya shiga Allah yasa de Ify, wasu chemicals ta hada hannunta dauke da test tube xataje laboratory tayi test da observation sannan tayi reporting tana fitowa a dab bakin kofa kicibis tayi karo da mutum test tube ya fadi chemicals na ckn tube din yayi splitting a kayan jikinsa. Imran ne ckn milk color suit nasa yayi kyau sosai Ruhaimat ta xare ido ckn matukar tsoro ko kwakwaran motsi ta kasa yi Allah ne kadai yasan abunda zai mata, ya kura mata ido ga mamakinta hawaye ta gani ya cika idanunsa dakyar ta bude baki tace "am..bata karasa bah ya juya ya koma ta bangaren da ya fito.bata ji dadin hakan bah tabbas tasan dole yaji haushinta duk da cewa ba da gayya tayi bah , Amma tasan lallai ransa a bace yake ckn sanyin jiki ta tattara test tube din nan masu aiki Suka fito ckn sauri suna gyara wajen..Ruhaimat tayi shiru ta rasa me ke mata dadi ta tashi ckn rashin kwarin guiwa , ofishin mr Ibrahim ta wuce kai tsaye ta shiga tare da sallama ya amsa mata "ahm...yaya na ka taimakamin ina ne ofishin sales director pls" "aw..imraN kike nem ki je next floor by ur right xaki shiga sales section daga nan xaki iya tambaya se a nuna miki" nagode" daga nan ta juya ta tafi Ibrahim ya lura da yanayinta ko meke damuntane oho!

Elevator ta shiga bayan ya sadata da sales dprtmnt gskiya floor din ya hadu komai nasu a tsare jama'a anata hrkoki. Ruhaimat bata sha wani wahala bah wajen Neman ofishinsa , kai tsaye ta bude tare da sallama katafaren office ne mai girman gaske tsarin kamar cki da falo ne nan ta bude wata kofar da ta gani. Yana nan kishingide a bisa kujera idonsa a rufe ya cire suit din ya ajiye a gefe "wat do u want" ya fada ba tare da ya bude ido bah "am sorry director... Ckn sauri ya bude ido yace "waat? Ke me kike nema me ya kawoki ofishina " ya fadi maganar ckn daga murya , ta marairaice tace "am very very sorry wllhi tsausayi ne am sorry pls" hmm sausayi? Sausayi fa kika CE? tsautsayin naki baxata afka akan kowa ba sai ni" kayi hakuri don Allah" ya tsaya yana kallonta yama rasa ya xaiyi da ita da karfi ya kwantar da kansa bisa tebur yana Jan tsaki, kamar a mafarki yaji sheshekar kukanta ya daga kai😳😳 hawayene cabe a fuskarta "hey malama mai hijabi me aka miki xaki fara min kuka ..pls leave kada wani ya shigo yayi tunanin cewa ni na saki kuka" ckn murya me rauni tace " don Allah kayi hakuri" ok fine ...na hakura just go" daga nan ta tashi ta fita yabi bayanta da kallo daga bisani ya ja tsaki haushin kansa yaji meyasa ya kasa yi mata fada , ransa a jagule haka ya tashi ya kulle offishin nasa ya tafi .

Har yamma ta koma gida tamkar Mara Ify haka ta kasance se xuwa dare Sadik ya kirata Suka sha hira sosai a nan yKe shaida mata gobe insha Allah suna tare" wani farin ckine ya lullubeta take ta manta da xncen bacin ran da take cki.bayan sun gama call din Ameena ne ya shigo ta daga "°haba kawata ina kika yasar da phn naki na kira har nagaji" sorry Ruhaimat wllhi bansan wayar a kashe take bah naje gidN biki ne daz y kika ji ni shiru" ba kin barni ni kadai bah I was so bored wllhi" eyya sorry kawata tuba nake" shikenan na hakura" tnx matar sadik" wow...😍😍 kin burgeni da wannan sunan da kika ambatA" haka Suka cigaba da hira har xuwa wani Dan lokaci sannan sukYi sallamA.
Ruhaimat ta kwanta da dimbin tunani a ranta.

*Reefat CE*😍😘😘
[1:58PM, 11/12/2016] +234 703 007 7024: 💞💞 *MAI SONA*💞💞
*14*

BY *Reefat yahya*

*nagode da kulawarku fans..masu turamin sakon gaisuwa ina amsawa tnx a lot Lov u all😘😘*

taimaka mata suka kimtsa gidan ko ina yayi fes sai qamshi ke tashi..tare suka yini har dare driver ya sauke su gida.tayi wanka ta shirya ckn wata sleeveless gown mai shegen kyau ga adon stones a gaban rigar ta baxa gashinta a kafada ga yan kunne fashion sai daukar ido suke tayi kyau ba kadan bah, kunun Aya take sha a yaynda idanunta na kan TV tana kallon wani Indian film ..ya shigo falon tare da sallama bata ji shigowarsa bah ya karasa kusa da ita qamshin turarensa ne yasa ta dago kanta nan suka hada ido, ajiye cup din tayi ta rungumesa sai kuma ta tura baki tace "ba ka tafi gun matarka ka barni da kewarka bah" dariya yake mata yace "oh..mata kishi, dsame tin sadee take fada..wai ya kuke so nayi da rayuwata" "shikenan sai ka koma wajenta ai" daga nan ta raba jikinta da nasa wai fushi take "am sorry pretty u know I Lov u" hawayene ya cika idanunta yayi saurin jawota jikinsa yana shafa fuskarta a hnkli yana cewa "pls bana son ganin hawayen ki kiyi hakuri plss..haba maini kinsan duk duniya babu macen da nake so sama dake, kuma rashinki ne yasa na auro wata ckn rashin Sani da kuma kaddara daga ubangiji..so ki kwantar da hankalin ki ke kadai nake so ok..." Haka ya cigaba da lallaba ta dakyar ya shawo kanta daga nan ya wuce dakinsa ya fada wanka ta taimaka masa ya shirya daga nan suka wuce dinning ta xuba masa abinci yana ci tana masa hira, yaci abincin sosai yana shan kunun ayar yana xuba santi yace "aw..dazu ina son na fada miki cewa kinyi kyau Amma rigimar yasa na manta" ta shagwabe fuska tace "ni fah bana rigima" "hmm..ke koh..idan ina tare dake kullum sai kin birkita min lissafi da wannan rigimar taki" bayan ya gama daga nan suka koma falo yana kallon news tana kwance kanta bisa cinyarsa yana wasa da suman kanta " my Dil!" "Na'am kismat" "ina xa kiyi service"  " duk inda suka tura ni" "a'a ba duka bah..ki xabi inda kike so xan nema miki" "ko ina ma matukar baxakayi nisa dani bah " murmushi yayi yace "daz my pretty" peck ya mata a goshi yace "I Lov u" ya kara wani saman hancinta yace "I want u" sai kuma Dora bakinsa saman nata nan suka fara kissing juna tamkar xasu cinye juna... Karar wayarsa ce ya katse Suda dakyar yasa hannu ya daga wayar sadee ce nan ya daga "hello sadiya" kuka ta fashe masa tana cewa "wayyo xan mutu don Allah kazo kada na mutu ban ganka bah..ina son ganinka kusa dani" duff ta kashe wayar hankalin sadeeq ya tashi ya juya yana kallon Ruhaimat "sadiya ce..ko haihuwar ce I don't knw cos wannan month nata ne" ya taashi ckn rawar jiki ya dauki makullin mota yace "sai na dawo" ckn sanyin murya tace " Allah ya bata lfy..takkia" daga nan sadeeq ya juya ya fita tabi bayansa da kallo can kasan xuciyarta kuwa wani zafin kishine ke addabarta gani take tamkar cin xarafi ne don tasan halin sadee tasan abunda xata iya aikata...

*Reefat ce*😘😘😘

*sorry pals gobe idan Allah ya kaimu baxan samu daman posting bah... Lov u all*
[4:55PM, 18/12/2016] +234 703 007 7024: 💞💞 *MAI SONA*💞💞
*67*
BY *Reefat yahya*

~an imaginary Lov story~

*godiya mai tarin yawa gareku masoyana tnx for d birthday wishes..Lov u all*❤❤❤

Zaune ya tarar da ita bisa kujera ta dora kafa daya bisa daya tasha makeup tayi shiga ckn wata arniyar nyt wear se zabga kamshi take ..sadeeq ya ja turus ya tsaya yana kallonta cike da jin haushi yace "ynxu kin kyauta kenan?.. Kinsan halin rudani da na shiga?..meyasa xaki min haka sadiya" murmushi take ta tashi ta rungumesa iska take hura masa a kunne sannan ta fara magana ckn salon yaudara "sorry swt hrt na daga maka hankali koh..nayi missing naka Shiyasa nabi wannan hanyar don kasancewa tare da kai" tsaki yaja ya raba jikinsa da nata yace "amma de kinsan gun Ruhaimat xan kwana koh" ta hada rai tace "wannan wane irin wulakanci ne haka..tare kuka dawo fah, kwana nawa kuka yi a can" nan ta fara kukan ckn kissa sadeeq ya runtse ido yace "ohh..mata 2 wahala" daga nan ya fara rarrashinta ya jawota jikinsa ya rungumeta..

***da safe misalin 11 Ruhaimat ta chaba ado tana xaune a falon sama sai duba agogo take ta cika tayi fam ..gaba daya haushinsu take ji tun jiya tana kiran layinsa baya dagawa , yayi parking ya fito ckn kasaita yasha farar shadda galila yayi kyau sosai ya duba dayan falon bata ciki don haka ya haura xuwa dayan falon..ya shigo tare da sallama can cki2* ta amsa masa daga bisani tace "ina kwana" murmushi yayi ya karasa kusa da ita hannunta ya rike yana murxawa "ya kika tashi my Dil..u luk gorgeous" ckn xuciyarta tace "munafuki kawai..xaka ji dashi ai" harara take carab suka hada ido tayi saurin dauke kai "harara ta kike maini" ta kauda kai gefe bata ce komai bah "am sorry ok..nasan fushin da kike duk bai.." Hannu da daga masa tare da cewa "akan me xanyi fushi?..don ka kwana gidan matar ka?" Shiru yayi yana kallonta..Ruhaimat akwai xafin kishi koda yake ba laifinta bane duk masu suna Aisha haka suke☺☺☺☺☺ amma fa ba kishin hauka bah..matured kishi😍😍👍🏼a hnkli ta tashi ta fara tafiya "ina zaki je" "abinci xan dauko maka" "amm..da kin barshi xuwa anjima " hawaye ne suka taru a idanunta ckn hanxari ya karasa inda take "haba maini..meyasa kike da saurin kuka ne, kin Faye shagwaba wllhi Abu kadan sai ki fara kuka...nidai Hajja ta hadani da aiki wllhi, sorry toh muje ki bani a baki ok" yana wani lallabata sai tirjewa take daga karshe ya dagata cak! Bai direta ko ina bah sai bisa dinning table.sai ririta ta yake a haka suka ci abincin shi yake bata a baki har suka gama yace "my Dil xan wuce office, batun kwana kuma na raba muku 2- 2days is ok ryt?" ta marairaice tace "ynxu duk girman gidan nan ni kadai xan xauna a ciki" nan ya jawota ya Dora kanta bisa kirjinsa yace " sorry pretty Nah hakuri xakiyi..ni kaina bana son kiyi nisa dani kawai ya xama dole ne" ta turo baki tace " nikam tafiya xanyi gidan anty Xee sai ranar girki na sannan na dawo" dariya yayi yana kallonta yace " oh..pretty rigima, yi hakuri ki xauna gidan mijin ki ok" "um..um nikam.." Bata karasa ba ya tura bakinsa ckn nata suka fara kissing din juna dakyar suka rabu ya tafi office cike da kewar ta.

*** _5days leta_...sadiya ta haifi baby girl kyakkyawa mai kama da sadeeq Amma tasha drips kam taji jiki sosai dakyar ta samu sauki aka sallamesu suka koma gida, Ruhaimat taje dubata tare da mata barka kallon banxa suka mata taso daukar yarinya Amma Sam sadiya taki amincewa..abun ya mata xafi ba kadan bah haka ta tashi ta koma gida cike da bacin rai don Ruhaimat akwaita da son yara kanana.haka suka kasance sadeeq ya dawo gidanta gaba daya safe da yamma yake xuwa gidan sadiya don duba lafiyarsu, kullum yana makale da Ruhaimat suna xuba soyayya son ransu.ranar suna yarinya taci sunan mami wato zainab baba da mami sunzo daga Abuja, a gidan mami aka hada kayan suna su Ruhaimat ne a gaba ga kuma meenah amarya sai sauran dangi anty maryam da anty Xee ma duk sunzo.bayan azahar aka kawo motoci suka kwashe mutane xuwa gidan suna wato can gidan sadiya, maijego tayi kyau

xagaye take da kawayenta en abi yarima asha kida sai hira suke suna ihu da shewa🙄🙄🙄 aikuwa ganin kwalliyar Ruhaimat yasa kowacce ta raina kanta har da ita sadee tasha jinin jikinta, nan aka gabatar da kayan uba da na dangi..wata akwati mai Karen kyau aka budeta super wax 2Holland 2 swiss lace 1 sai kayan jarirai kala 10 da sauran tarkace irin su pant..bbypowder..bbysoap da sauransu kayan sun hadu kowa ya baxa ear don jin daga ina kayan suka fito , meenah tayi gyaran murya tace" ga kayan step mom nata wato Ruhaimat"😳😳 ba sadee kadai bah duk jama'an dake wajen sunyi mamaki..jikin sadee yayi sanyi dakyar ta bude baki tayi godiya Ruhaimat dai ko kallonsu bata yi bah hasali ma chat take da masoyin nata kowa sai kallonta ake.

*Reefat ce*😘😘😘😘
[4:56PM, 18/12/2016] +234 703 007 7024: 💞💞 *MAI SONA*💞💞
*68*
BY *Reefat yahya*

*an imaginary Lov story*

Bayan suna da sati 2 akayi bikin imran tare da amaryarsa yasmeen ango dai daurewa kawai yake Amma fuskarsa babu alamar walwala amaryar ce ke shige masa ita kam fuska kamar gonar auduga murna take Yau burinta ya cika, a wajen dinner ne suka hadu da Ruhaimat yayi saurin dauke kai da yake har Yau Ruhaimat bata San cewa ya fada sonta bah tare suke da sadeeq sunyi kyau sosai duk inda suka wuce sai kallonsu ake sun karasa gun ango da amarya don tayasu murna.fuskar Ruhaimat dauke da murmushi tayi wa yasmeen magana harara ta galla mata ba tare da ta amsa bah, bata damu bah don haka ta juya gun imran "dosti congrats Allah ya bada xaman lfy" dakyar ya amsa da "ameen " ba tare da ya daga ido ya kalleta bah taja bakinta tayi shiru a haka aka gama program kowa ya kama gabansa.
****kwanci tashi ba wuya gun Allah..result din su Ruhaimat ya fito ta fita da sakamako mai kyau an fitar da list din nysc sunanta na ckn first batch tsabanin sadee , wani kishi ne ya turnuketa tana jin haushin Ruhaimat.. A nan yola ta fara serving ckn kwanciyar hankali tayi bulbul da ita ta kara kyau ba kadan bah a wannan lokacin ne anty maryam ta haifi danta namiji a jada akayi suna inda Ruhaimat ta taka muhimmiyar rawa kowa na alfahari da ita, bayan suna ta kara kwana 2 sannan sadeeq yaje ya dauketa suka dawo yola.sadiya tayi jiki sosai ga jaririyarta wacce suke kira da Mimi ita ma bulbul gwanin sha'awa yarinyar sai kara kyau take kamanninta da na sadeeq sai kara bayyanowa yake.ynxu wata 5 take dashi Amma tayi jiki xaka dauka cewa tayi shekara 1 da rabi , Ruhaimat na matukar kaunarta Amma Sam sadiya bata barinta ta rike yarinyar tun bayan suna kafa har 5 tana xuwa Amma ko sau daya bata samu damar daga ta bah.wata rana idan ta koma gida takanyi kuka Amma bata taba nunawa sadeeq komai bah gashi ita har ynxu shiru babu ciki ba alamarsa, idan tayi magana sadeeq ne ke nuna mata komai lokaci ne yana matukar kyautata mata yana bata kulawa fiye da komai a rayuwarsa.Yau weekend tana kitchen tana hada musu breakfast daga ita sai wata er Riga mai guntun hannu da kuma bone Short ta tufke gashin kanta a baya ta gama shirya komai tana yanka fruits ne don al'adar sadeeq kenan ko wace safiya sai ya sha fruit salad..rungumarta yayi ta baya yana shakar daddadan qamshin turarenta hannunsa xagaye da kuguntra "morning my

Dil..kina ta aiki ke kadai baxaki tasheni na tayaki bah" murmushi tayi tace "nasan ka gaji daz y na kyaleka ka huta..hw was ur nyt" "uhmm...it was splendid ,wit u by mah side I don't have any prblm" "daz grt" ya fara shinshinata kamar wani tsohon maye🙄🙄 tace "haba kismat..wuka ce a hannuna fah" "I need u Dil.." Ta turo baki ckn shagwaba tace "um..kana ganin aikin da nake" peck ya mata a wuya yace "gskiya ki bar aikin nan muje..am hungry" "toh ba ga abinci a nan bah" "ni ba wannan nake bukata bah..kingane me nake nufi ai" dariya tayi ta ajiye wukar ta karasa kusa da sink tana wanke hannunta cak! Ya dagata suka fita daga kitchen din tun a nana ya fara kissing nata dakyar yake tafiya yaga baxai iya xuwan daki da ita bah don haka ya shimfideta bisa kafet din falon , tamkar xasu hadiye junansu nan ya bude buttons din rigarta suka cigaba da abunda suke dai2* nan suka jiyo door bell tsaki sadeeq yaja dole ya tashi a wahale maballalan rigansa duk a bude ga kirjinsa nan a waje ya karasa bakin kofar yana cewa "waye " ya bude kofa suka hada ido da sadee tana tsaye ga Mimi nan rungume a da ita "lfy sadee dis early morning" harara ta galla masa tace " 10am kake cewa early..bani hanya dallah ni xiyara nazo" "da izinin wa" ta tabe baki tace "au..nan dinma sai na nemi ixini ne? Gani nayi da nan da can duk dayane" daga nan tasa kai tayi shigewarta ya kulle kofar tare da bin bayanta yana jin haushinta..turus! ta ja ta tsaya ganin kayan dake jikin Ruhaimat kuma ga nan kirjinta rabi duk a waje, ta maida dubanta gun sadeeq daga nan tsaki taja tace "jarababbu sai aje ayi wanka ai" murmushi Ruhaimat tayi tace "barka da xuwa maman Mimi..sorry bamuyi expecting bako a wannan lokacin bah Shiyasa kika samemu haka" nan ta tashi tana kallon sadeeq tace "kismat muje na ma wanka koh" "ok my Dil let's go" ta kwanta a jikinsa ya dagata tamkar karamar yarinya suka haura saman bene sadee ta bude baki da hanci tana kallonsu.bayan tafiyarsu ne ta dawo hankalinta tana bin gidan da ido tabbas ynxu ne ta yarda da abunda ake gaya mata na cewa gidan Ruhaimat yafi nata nesa ba kusa bah dama abunda taxo gani kenan... Lallai yarinyar nan irin wannan dankareren gida haka? Dole ta tashi tsaye tayi wani Abu idan bahaka bah Ruhaimat xata rabata da sadeeq..anya bokan nan yayi aikin da na sashi kenan🤔🤔🤔 dole ta koma gun boka.haka dai ta cigaba da tunani har suka fito sunyi kyau sosai daga nan Ruhaimat ta shirya abinci bisa table, Mimi na hannun babanta yana mata wasa Ruhaimat ta xuba musu abinci sadee kam sai kallonta take..abinci kala 5 ne pancakes awara fish rolls chips da fried indomie da kwai sai tea da kuma fruit salad. Sadeeq yasa spoon ya deba fruit salad xai kai bakinsa Ruhaimat ta rike hannun tace "hot first" murmushi yayi daga nan ta tura masa filet din indomie da kwai, da zafinsa haka yake ci sadee na kallonsu tana mai jin haushi. Bayan azahar ta bar gidan Mimi tasha kyaututuka daga wajen Ruhaimat, gidansu ta nufa dama da motarta taxo bayan ta ajiye Mimi gun innarta tace xata je unguwa daga nan ta fita.gudu take sosai xuciyarta na tafarfasa cike take da haushin Ruhaimat burinta kawai taje gun boka a raba Ruhaimat da sadeeq rabuwa ta har abada..wata trailer ce sukayi karo ba tare da saninta bah don hankalinta baya kan hanya, motar sadee ta nausa ckn daji a nan driver yaja birki..jama'a sukayi caa..suna nanata "innalillah😱😱😱

*Reefat ce*😘😘😘😘
[11:38PM, 19/12/2016] +234 703 007 7024: 💞💞 *MAI SONA*💞💞
*70*
BY *Reefat yahya*

~an imaginary Lov story~

*Lov u all  ..happy reading*❤❤❤ _Reefat tana sonku_😘😘😘

Bayan kwana 2 Ruhaimat ta nemi su koma asibiti duba lafiyar sadee amma firr sadeeq yaki amincewa haka nan bai shaida mata cewa ya saki sadiya bah..haka ta hakura ta cigaba da kula da Mimi tamkar ita ta haifeta yarinyar ta fara sabawa da Ruhaimat. Bayan wata daya aka sallami sadee daga asibiti suka koma gida daga nan kannenta sukaje gidan sadeeq suka kwashe kayan sadee a wannan ranar ne Ruhaimat taji labarin sakin tayi fada sosai haka ta sashi a gaba tana masa fada tamkar ita ta haifesa yayi jugum yana kallonta sai da ta gama fadan nata sannan ya dauki makulli ya fice ya bar mata gidan, kwana 3 sukayi suna fushi da juna gaisuwace kadai ke hadasu dukkan su suna ckn damuwa suna kewar juna ba kadan bah haka suke daurewa.xaune take a falo ta kwantar da Mimi bisa cinyarta tana wasa da suman kanta da ya fara fitowa sadeeq yana xaune a can gefe yana kallon news Amma jefi2* yana satar kallonta.wayarsa ce tayi ruri ya daga "hello mamina" shiru yayi yasha jinin jikinsa don fada take masa tamkar xata bi ta ckn wayar ta samesa..sun share 30mins tana fada sadeeq dai sai hakuri yake bata don fada take masa akan sakin sadee da yayi jiya ta samu labari gun masu aikin gidan daga karshe tayi hanging call din, shiru yayi ya juya carab! Suka hada ido da Ruhaimat ya bata tausayi don shima Dan uwan dayar ne akwai shagwaba kuma baya son fada..ya marairaice tamkar xeyi kuka "my Dil kina ganin mami tayi fushi dani koh" murmushi tayi ta kwantar da Mimi daga nan ta koma kusa dashi ta xauna "com hre" ta bude hannayenta nan ya fada jikinta ta rungumesa ya kankameta sosai tana shafa gashin kansa tace "kismat baka jin magana n wat u did is wrong dole mami ta nuna maka fushinta..sorry koh is ok" ajiyar xuciya yayi tare da cewa "bayan kema kina fushi dani kin daina kulani" "ohh..c'mon is ok" peck ta masa a goshi sun Dade a ckn wannan yanayin daga karshe suka fada wata duniya daban.
**** _ina labarin ango imran ne??_ zaman nasu babu canji imran baya shiga sabgar yasmeen ita ko tabi ta damu baya kulata ko kadan haushinta yake ji don babu abinda ta iya komai masu aiki ke mata abu yaki ci yaki cinyewa dole yasmeen ta tattara ta koma gidan momin imran ta kai kararsa tace lallai baxata koma gidansa bah sai ranar da ya canza hali, imran kam bai damu bah haka ya cigaba da harkokinsa Ibrahim ma suna xaune lfy da meenah ynxu haka tana fama da tsohon ciki haka nan Ameena Mrs Aliyu jada.haka Rayuwa ta kasance akwana a tashi Ruhaimat ta gama bautar kasar da take ranar da xasu gama mami da baba sunzo tayata murna haka nan mutanen gidansu babu Wanda bai zo bah..umma Abba ya Yusuf anty Xee anty maryam da sauransu babu Wanda Ruhaimat tayi murnar gani kamar Hajja Dada , ranar ta rasa inda xata sa kanta don murna gaba daya sun nuna farin cknsu mami da baba sun jajanta mata dangane da labarin abunda sadee ta mata haka nan suka bata hakuri da karfin guiwa.bayan an watse daga taron gida suka wuce gaba dayansu meenah da Ameena duk sunzo, sun yini tare a gidan Ruhaimat abinci kala2* suka ci har xuwa dare sauran suka koma gidajensu aka bar umma Abba Hajja Dada da kuma Ameena su a nan zasu kwana.dakyar su umma suka amince don tsabar kunya nan Ruhaimat ta gyara musu dakuna daga nan sukayi sallama sun wuce don yin bacci, dakinta ta gyara ma Ameena daga nan ta koma dakin sadeeq fitowarsa daga wanka kenan nan itama ta wuce ta fada wankan bayan ta fito ta shirya  suka kwanta don Mimi tana

gun mami.
    Da safe ta shirya musu breakfast tare suka karya da sadeeq da Ameena, da wuri su Abba suka shirya don komawa ya Yusuf ne yaxo daukarsu don ba nan ya kwana bah a can gidan hajiya maryam ya kwana.duk yanda Ruhaimat taso Hajja Dada ta xauna da ita fafur sunki amincewa dole ta hakura sukayi sallama suka tafi tare da Ameena. Da yamma mami ta shirya tare da Ruhaimat driver ya kaisu gidan su sadee mami na bin gidan da ido lallai suna ckn talauci, ckn mutunci inna ta karbesu ynxu tayi hankali ta koyi darasin rayuwa tayi sanyi kamar ba ita bah...sadee na ganinsu ta fashe da kuka Ruhaimat ma kukan take mami ce ke basu hakuri sadee tana kallon Mimi ta kara fashewa da kuka, sun Dade a gidan daga bisani mami ta ajiye musu kudade masu yawa tana bada hakuri akan sakin da sadeeq ya mata sannan suka fice daga gidan. Maimakon su koma gida gani tayi sun dau wata hanya daban gidan Alhaji sultan sukayi parking Ruhaimat ta fito tabi bayan mami.

*Reefat ce*😘😘😘😘
[11:39PM, 19/12/2016] +234 703 007 7024: 💞💞 *MAI SONA*💞💞
*71*
BY *Reefat yahya*

~an imaginary Lov story~

❤❤❤ _Reefat tana sonku_😘😘😘

Sun shigo falon tare da sallama, imran ya fito zai wuce masallaci kenan ya daga kansa suka hada ido da Ruhaimat yayi saurin dauke kai yace "mami barka da xuwa Ku karasa suna ciki" yayi wucewarsa Ruhaimat de tana mamakin sauyin da yayi bahaka ta sanshi bah..Momi tayi farin ckn ganinsu a nan sukayi magrib sannan suka koma falo suna hira yasmeen ta shigo tare da sallama tana cewa "wash..Momi na gaji wllhi nayi rawa Yau ba kadan bah" tsaki Momi ta ja tare da cewa " Allah ya shirya.. Ki jira mijin naki don ya shigo yana tambayar ki, dama karya kika min da kika ce shiya baki izinin xuwa gidan bikin" dariya tayi sai ynxu ta kula da su mami tace "lah..Momi baki mukayi" "Mara kunya..wannan mahaifiyar sadeeq ce tare da matarsa" murmushi tayi "ina yinin Ku" mami ta amsa ckn sakin fuska , Ruhaimat ta juya kenan suka hada ido yasmeen ta bude baki cke da mamaki tace "ahh..wannan ce matar sadeeq?, amma ai ba ita bace wacce na Sani" "amaryar sa kenan sunanta Ruhaimat" tabbas yasmeen tasha ganin hotunan Ruhaimat ckn wayar imran kuma ta San cewa imran yana matukar kaunar Ruhaimat.. Amma mamakinta shine yanda ta canza ta kara kyau ga kuma dressing nata mai daukar hnkli ..sabanin da ta Santa da hijabi tana mata kallon bagidajiya, da wannan tunanin ta wuce dakin Momi "hajiya mami kina ganinta ai..haka nake fama kullum gani nan sai raba fada, wllhi nagaji abun nasu baya karewa" mami tace "meya kawota nan gidan bayan ga gidan mijinta" "wllhi bata da hankali ko kadan iyayenta sun sangartata..ni tausayin imran nake ji hakuri kawai yake ya xuba mata ido" "gskiya kiyi kokari ki wayar mata da kai don na lura tNa ckn duhu batasan ya ake rayuwar aure bah..kina cutar da danki a banxa ga mata nan birjik meyasa kuka xaba masa wannan fisararriyar" "uhmm kedai bari kawai..xanyi bakin kokarina" "Allah yasa mu dace" wayar

Ruhaimat ya sake vibrating a karo na 5 murmushi mami tayi tace " chewing gum naki koh..nasan yana can yana jira tashi mu tafi" Momi tayi jugum tana kallon Ruhaimat.. Allah sarki imran da Ibrahim sunyi rashin mace ta gari .."toh Momi imran mun tafi" "nagode kawata Allah ya bar xumunci..dota nagode koh" daki ta wuce ta fito dauke da wata bakar Leda ta mikawa Ruhaimat dakyar ta karba tare da yin godiya daga nan suka wuce gida.
Sati 1 su mami sukayi daga nan suka koma Abuja tare da Mimi Ruhaimat tayi kewar yarinyar sosai don ita take kipin nata busy...wata sabuwar rayuwar soyayya suka shimfida tamkar xasu hadiye juna tare suke yin komai idan yana office ma suna makale da juna a waya haka Rayuwa ta cigaba suna rokon Allah akan samun haihuwa don har ynxu shiru kake ji kamar an shuka dusa.xaune yake bisa carpet grass a yayinda Ruhaimat tayi matashi da cinyarsa a garden din gidan suke suna shan iska tana karanta masa littafin *kissoshin annabawa* yana jin dadin tarihin annabi Yusuf da take karanta masa sai faman lumshe ido yake, Momi ce tare da yasmeen suka shigo masu gadi suka shaida musu inda masu gidan suke kai tsaye wajen garden suka nufa yasmeen na raba ido tana mamakin girma da kyawun gidan saboda bata taba xuwa bah gidan da sadee ta xauna ne taje sau 1.sadeeq ne ya hangosu yace "maini munyi baki tashi ki xauna" ckn sauri ta tashi ta sanya hijabinta don kananan kayane a jikinta "lah..Momi Yau kece a gidan namu..barka da xuwa" ckn tsananin kunya Ruhaimat ta musu maraba , sadeeq yace "mu je ciki koh" daga nan suka koma ckn gida a falo suka xauna Ruhaimat ta jera musu kayan motsa baki bayan sun gaisa sadeeq ya tashi ya fita Ruhaimat tabi bayansa a bakin motarsa ya tsaya nan suka rungumi juna ya manna mata peck a kumatu yace"ki kula kanki idan sun tafi ki kirani ok.." "Ok..u too takkia" "Lov u" "Lov u more..banda kallon mata" murmushi yayi tare da cewa "ni me xan kalla a jikin wata mace..I have u I have everything" murmushin jin dadi take daga nan ta daga masa hannu yaja motarsa ya tafi.duk abunda sukayi akan idon yasmeen mamaki ne karara a fuskarta..dama haka Ruhaimat ta iya soyayya? Yaushe ta waye haka? Xama tayi bisa kujera tana bin falon da ido har taji ta raina kanta..ikon Allah kenan wai Ruhaimat ce ckn wannan katafaren gida haka?, koda Ruhaimat ta shigo yasmeen bata daina kallonta bah..minti 50 sukayi a gidan sannan suka mata sallama.. Cake doughnut da kunun Aya ta xuba musu ckn bakar Leda sai kayan makeup da turarukan humra masu kamshi ta rakasu har bakin mota ta ajiye ledojin a gidan baya godiya sukayi yasmeen ta ja motar sika koma gida. Momi ta kula da halin da take ciki tun bayan dawowarsu daga gidan Ruhaimat "yasmeen meke damunki na ga kin xama wani iri" "Momi magana zamuyi" "ok go ahead"......

*Reefat ce*😘😘😘😘
[9:26PM, 20/12/2016] +234 703 007 7024: 💞💞 *MAI SONA*💞💞
*73*
BY *Reefat yahya*

~an imaginary Lov story~

Baba ya kira ya sanar dasu akan cewa visa dinsu ya fito daga nan Ruhaimat ta xaga danginta na ckn yola da jimeta sannan suka wuce jada a nan tayi kwana 3 tayo sallama da iyaye da en

uwanta suka dawo yola washe gari jirginsu ya daga xuwa Abuja, mami tayi murna kwarai da gaske meenah tana can ta koma sai bayan ta haihu xata dawo gidan minjinta.mimi ta girma tayi wayo ga jiki bulbul gwanin sha'awa tana ganin Ruhaimat ta fara dariya Ruhaimat ta dauketa tana mata wasa, bayan kwana 2 da xuwansu suka cigaba da shirin tafiya don saura kwana 3 tafiyar tasu.Ruhaimat dauke da Mimi tana mata wasa sai dariya take kyalkyalewa a falon mami suke mamin na xaune a gefe tana kallonsu a can kasar xuciyarta kuwa tausayin Ruhaimat ne ya kamata ..tana mata adua Allah ya bata haihuwa Allah ya axurtata da ya'ya masu albarka, sadeeq ya shigo da sallama ckn shigar kananan kaya yayi kyau sosai Ruhaimat na satar kallonsa.kusa da ita ya xauna yasa hannu xai dauki Mimi yarinyar taki amincewa ta kara makalewa Ruhaimat, dariya mami da Ruhaimat sukayi sadeeq ya marairaice yace "mami kina ganin yarinyar nan..tun shekaran jiya fah taki amincewa na daga ta" "toh ba sai ka hakura bah malam" ya bata fuska kamar xeyi kuka Ruhaimat ta fakaici idon mami ta masa gwalo nan ya kara harzuka "mami kina gani tana min gwalo" "wa kenan?" Haushi yasa ya bar musu falon suna masa dariya. Ruhaimat tace " Allah mami kin shagwaba ya sadeeq dayawa" murmushi mami tayi tace "wato kin koma team din su meenah koh" dariya tayi tace "aa mami's team nake" meenah ta shigo rike da pancakes a plate murmushi Ruhaimat tayi tare da cewa "acici's" tsaki meenah taja tace "sanin kanki wllhi larura ce don da bahaka nake bah" dariya mami take musu "haba mami dariya kke xaki min " " meenah me xan miki" ta bata fuska tace "dama ai anty Ruhaimat bata laifi" mami ta tashi tsaye tace "kinga tafiyata don nasan wasu abubuwan kuna yine don ganin idona" daga nan ta fice tana dariya, Ruhaimat ta matso kusa da ita tace "haba mutuniyar kinsan nida ke mutu ka raba..wasa nake miki my meenah" murmushi meenah tayi tare da cewa "lokacine yarinya.. Ai naki na nan tafe" hira suke sosai meenah na jajanta batun sadee , sadeeq ya shigo yace " lallai maini..kina ganin mijinki yayi fushi ya tafi Amma kin kasa xuwa ki bashi hakuri kin xauna kina biyewa wannan mai surutun tsiya koh" "hmm..su miji manya" meenah ta fada tana dariya nan Ruhaimat ta sauke Mimi bisa cinyar meenah tace "xauna a nan my bby kinsan baban naki Dan rigima ne" murmushi yayi ya jawota suka jera suna shirin barin falon meenah tace "oh..antyna babu ko kunya" "babu harkar kunya yarinya..ke waya San me kike yi a gidan naki" dariya sukayi gaba dayansu nan suka wuce bangaren su. Da yamma suka shirya sadeeq ya daukesu a mota suka fita yawo tare da Mimi da kuma meenah basu dawo gida bah sai xuwa dare, haka suka kasance ckn kwanciyar hnkli har xuwa ranar da xasu tafi gaba daya familyn suka dugunxuma xuwa airport dakyar aka raba Mimi da Ruhaimat ta makalkale a jikinta da aka rabasu kuwa ta fara kuka nan hawaye suka cika idanun Ruhaimat a haka suka shiga jirgi tana xubda hawaye, sadeeq ne ya daura mata belt ya kwantar da kanta a kafadarsa yana faman rarrashinta dakyar ya samu ta daina kukan daga nan jirginsu ya daga✈✈✈✈don xuwa Saudi arabia d most wonderful country.

******* sun sauka Ify hotel ya kama musu kafin ya nema musu inda xasu xauna permanent, bayan sunyi sallah sun huta ne ya kira iyayensu ya sanar dasu sun iso Ify daga nan suka fada wanka.tare suka shirya nan suka hau gado kanta na bisa kirjinsa haka sukayi bacci mai dadi.

Haka Rayuwa ta kasance Ruhaimat ta fara xuwan makaranta fannin addini take karantawa haka nan sadeeq ya fara xuwa PhD classes nasa a garin jeddah, rayuwar so da kula tare da mutunta juna sukayi duk Wanda ya kallesu dole yaji sun burgeshi kowannensu ya maida hankali sosai gun karatun da suke..a kwana a tashi ba wuya gun Allah Yau sun share shekara 2 a kasar saudiya nan suka fara shirin xuwa ganin gida.Ruhaimat tayi kyau tamkar a saceta a gudu har

Yau babu labarin ciki kuma daga shi sadeeq har iyayensa babu Wanda yasa damuwa a ransa basu fidda tsammani bah a ganinsu komai lokaci ne Mimi ta girma sai shegen surutu,yaran meenah 2 duk mata haka nan yasmeen ta haifi danta namiji Ameena Aliyu na da yara 2mace da namiji.sati 2 Ruhaimat tayi a jada tayi mamakin ganin sabon ginin da aka musu Hajja Dada tsohuwa mai ran karfe ita ta fada mata cewa baba ne ya bada kwangilar gidan tsakaninta da surukan nata sai godiya taje xiyara a can yola yasmeen ta karbeta da hannu biyu, haka nan taje gidansu sadee Allah sarki Rayuwa tana kwance sai abunda aka mata ta xama abar tausayi..duniya kenan ( mohulai Allah semti😟😟).

*3 years leta* xaune take bisa gadonta mai alfarma a can madinatul munawwara katon ciki ne da ita sai marairaice cewa take sadeeq yana xaune yana faman ririta ta "haba maini ina xaa samo saki a nan garin" kamar xatayi kuka tace "ni nasan bara'a rasa bah kawai ni faten saki xanci😫😫 " ta karashe maganar tana kuka gaba daya ya rikice haka yake fama da ita tunda ta samo ckn bata son yayi nisa da ita ga kuma kwadayin tsiya..ynxu ckn Nada wata 6 .ya gama PhD dinsa ita kuma tana final year nata tana hada masters don tayi degree ta gama ynxu tana kan masters, tayi xurfi ckn karatu sosai addini ya shigeta ba kadan bah don tana da kwazo sosai ynxu haka ana inviting nata conference ko seminar a gararuwa daban2* ckn fadin kasar.haka sadeeq yake fama da shagwaba sai lallabata yake kamar kwai har Allah yasa ta sauka Ify ta haifi danta kamar Dan larabawa, baba mami umma Abba Hajja Dada meenah Ibrahim imran yasmeen da kuma momin imran su suka zo suna yaro yaci sunan Abba wato Abubakar😍😍.. Abubakar Dan Abubakar jikan Abubakar👍🏽👍🏽 bayan suna sukayi aikin hajji gaba dayansu sannan suka dawo 9ja..

*Reefat ce*😘😘😘
[9:27PM, 20/12/2016] +234 703 007 7024: 💞💞 *MAI SONA*💞💞
*72*
By *Reefat yahya*

~an imaginary Lov story~

A hnkli yasmeen ta fara magana da cewa "Momi ina son komawa gidan ya imran Amma baya sona bansan ya zanyi bah..don Allah ki taimakeni wllhi ina matukar son ya imran , baya sona har ynxu yana bakin ckn rabuwa da Ruhaimat Shiyasa bana gabansa" "kiyi hakuri yasmeen.. Shi namiji tamkar jariri yake ke xaki koya masa komai tun da farko , amma rashin ilimin xamantakewar aure shiya jawo miki wannan matsalar...is not too late zaki iya gyarawa" ta gyara xama tace "Momi ya xanyi? Wllhi a shirye nake zan iya aikata komai don jawo hankalinsa" murmushi Momi tayi tace "Abu daya zaki yi" "menene wannan abun " "gidan Ruhaimat xaki koma ita xata koya miki duk abunda ya dace na tabbata xata wayar miki da kai" "Allah Momi kunyarta nake ji don naci xarafinta a da can baya " "kada ki samu damuwa..Ruhaimat yarinya ce mai hankali na tabbata xata taimaka miki" "shikenan Momi hakan xaayi " "kwantar da hankalinki gobe xan kirata a waya xan sanar da ita komai" "nagode Momi..wllhi baki ji yanda suka birgeni bah Yau da muka je gidan, gskiya Ruhaimat tayi dace a duniya " haka dai yasmeen ta cigaba da xancen Ruhaimat. Kamar yanda suka tsara hakan ta kasance da safe Momi ta kira

Ruhaimat sun Dade suna magana daga karshe sukayi sallama nan ta kira driver ya sauke yasmeen gidan Ruhaimat don xata fita da motar saboda yasmeen bata taho da tata motar bah.

Sadeeq ya tafi office don haka Ruhaimat ta gyara gidan ko ina fes tayi wanka ta fito ckn ado na alfarma tamkar mai shirin xuwa gidan biki, yasmeen ta shigo tare da sallama cike da kunya Ruhaimat ta karbeta hannu bibbiyu bayan sun gaisa ta kawo mata kayan marmari bata ci bah nan Ruhaimat ta gane cewa yasmeen na jin kunyarta bisa abubuwan da suka faru tsakaninsu, murmushi tayi tace "haba yasmeen ki daina jin kunyata ki daukeni tamkar kanwarki uwa daya uba daya sannan kuma aminiyarki mai fatan ganin farin cknki, ina so ki mance da duk abubuwan da suka faru a da can baya" yasmeen ta sunkuyar da kai tace " kiyi hakuri nayi hakan ne bisa kuskure da zafin kishi saboda ina matukar kaunar imran Amma har Yau na kasa samun soyayyarsa, xuciyarsa na can wani waje yana dawainiya da son wacce bata San yana yi bah" "kina nufin ya imran wata yake so ba ke bah" cike da mamaki yasmeen ta daga kanta tana kallon Ruhaimat tace "tabbas..imran baya kaunata imran yana fama da ciwon sonki Wanda har abada baxai iya cirewa a ckn xuciyarsa" shiru sukayi suna kallon juna..rayuwar da sukayi tare da imran ya fara dawo mata a kwakwalwa..tabbas imran mai kaunarta ne Amma meyasa bai taba furta mata bah?? Take taji tausayinsa ya kama ta..Allah sarki dosti..Ashe haka yake fama da ciwon so kamar yanda ta fama lokacin da ta rasa sadeeq, lallai dole ta fidda shi ckn wannan halin ..hawayene suka cika idanunta tace "yasmeen ki min alkawari xaki dasa kaunar ki a ckn xuciyarsa xaki mantar dashi sunana a ckn rayuwarsa..xaki sa ya manta da duk wata alakar da ta taba faruwa tsakanina dashi, idan kinyi alkawari ni kuma a shirye nake da taimaka miki" "na miki alkawari insha Allah xan saye xuciyarsa ya fara sona Amma baxan miki alkawarin cewa imran xai manta dake a ckn xuciyarsa bah..don nasan hakan baxai taba faruwa bah" numfashi ta ja sannan ta fara magana " yasmeen ina son ki Sani cewa xuciyar Dan Adam kamar miyace wadda akayi mata shiri na musamman don tayi dadi ko abarta haka taki yin dadi, kamar yadda tsiro yake nuna abunda aka shuka shi xaa girba..haka rayuwa take don haka ya xama dole mu kula da addininmu da lafiyarmu da kuma mazajen mu..idan har kina Neman soyayyar mijinki dole ne ki San wadannan abubuwan: da farko ki kasance mai tsafta... mai gaskiya..ladabi da biyayya..iya kwalliya..iya girki ..girmama iyayensa da karrama danginsa...iya magana..ki kasance mai hakuri..kibi umarninsa..iya tafiya, murmushi, shagwaba da sauransu" a takaice dai yasmeen ta yini a gidan Ruhaimat har yamma sannan driver yaxo ya dauketa suka koma gida.

Ta gama tsara kwalliya tana jiran dawowarsa bayan wasu yan dakika taji tsayuwar motarsa nan ta tashi xata fita sukayi arba a bakin kofa ya dagata sama tamkar baby yana juyata dakinsa ya wuce da ita bai direta ko ina bah sai saman gado sannan ya fada gefe "washh..nagaji my Dil " sumbatar goshinsa tayi tare da cewa "sorry mai sona..muje kayi wanka ka ci abinci ka huta sannan na maka tausa" ya tashi xaune yace "da gaske ??..oh my pretty kinsan I Lov ur massage ai" gira ya daga mata murmushi take ta gane meyake nufi daga nan ta bude fridge ta dauko masa exotic mai sanyi ya karba yayi sipping kadan ya mika mata ta ajiye yace "Allah ya miki albarka maini..I Lov u so much" "Lov u more my Dil" ya jawota ta fada jikinsa yace "akwai albishir da xan miki Amma sai kin min wanka xan gaya miki" dariya tayi tace "toh muje mana...wannan dai baxai hada fada bah" daga nan suka wuce toilet tare.

_40mins leta_...yana kwance rub da ciki tana masa tausa " pretty kinsa nayi overfeeding gashi ynxu kasala nake ji" murmushi tayi "shine mai kyau kenan.. Kullum haka xaka yi dama baka son cin abinci ynxu dura xan maka every day" dariya yake sosai "aw..wayo koh! Ban manta ba ai

..albishir da kace xaka min" "ohh..hakane har na manta wllhi, sorry dawo nan kusa dani" babu gardama ta kwanta dab dashi tare da kura masa ido "ihmm..ki shirya goron da zaki bani" "a shirye nake sir!" Dariya ta basa , hannu yakai yana shafa Dan karamin bakinta yace "na fadawa baba dream naki na xama international scholar , dazu ina office ya kirani yace ya sama miki admission a garin madina tare xamu tafi ni xanyi PhD Nah a king Abdullahi university of science n technology jeddah" wani irin ihun da Ruhaimat tayi ta kankame shi tamkar xata shiga ckn jikinsa.dariya kawai yake mata "nagode..nagode..nagode *mai sona* Allah yabar kauna Allah ya kara budi da bunkasar arxiki, tnx I Lov u so much" godiya take masa daga karshe ta fashe da kukan farin ciki nan ya fara share mata hawaye, wani killer kiss ta masa tace "wannan shine goron " dariya yake yace Sam bai amince bah haka ta kira baba da mami ta xuba godiya daga nan ta fara kiran yan uwa da abokan arxiki tana sanar dasu.har Abbanta saida ya kira baba ya nuna godiyarsa a wannan Daren ta farantawa sadeeq rai ba kadan bah, washe gari suka hau shirye shiryen tafiya.

*Reefat ce*😘😘😘
[9:28PM, 20/12/2016] +234 703 007 7024: 💞💞 *MAI SONA*💞💞
*74*
BY *Reefat yahya*

*an imaginary Lov story*

Bayan wata 4 Ruhaimat ta kammala karatunta suka dawo Nigeria tare da kyakkyawan little sadeeq mai kama da Ruhaimat sak babu inda ya barota sai hasken mahaifinshi da ya dauka yaron yana kyau mai firgitarwa ga uwa uba farin jini Abba suke kiransa gashi da girman jiki, tunda suka dawo mami ke rawar jiki da jikan nata ta daina kula Mimi ba kamar da bah wannan ne yasa Mimi ta fara jin haushin kanin nata. WatA 1 da dawowarsu Ruhaimat ta fara rashin lfy bata iya cin abinci tea kadai take sha sadeeq yayi ta rokonta suje asibiti taki amincewa mami dai dariya take musu don ta gane ciki da ita abunka da manya kenan. Dole ya hakura yana lallabata dakyar take iya cin abinci idan taci kuma amai ne zai biyo baya ta share sati 2 ckn wannan halin wata rana meenah taxo ganin gida bayan sun kadaita a daki tace "ke anty Nah kice mu fara shirin xuwa suna man" ta xare ido " bangane bah" murmushi meenah tayi tace "u min baki San kina dauke da juna biyu bah"😳😳 wat?..juna biyu?, watannin Abba 6 fah" "oho..ke kika San wannan " Ruhaimat tayi rau2* tamkar mai shirin kuka "na shiga uku meenah ya xnyi" "ya xakiyi kuma sai hakuri Allah ya raba lfy" wayarta ya hau ruri Ibrahim ke kira don haka ta gyara kwanciya suka fara waya da mijin nata Ruhaimat tayi jugum tana tunani daga karshe ta tashi ta koma dakinta kwanciya tayi ta fada duniyar tunani, sadeeq ya Dade da shigowa bata Sani bah har ya karasa kusa da ita ya shafa gefen fuskarta nan ta tashi a firgice.."wats wrong maman sadeeq" nan ta fashe da kuka " kismat na shiga uku..Ashe duk rashin lfyn da nake yi ciki ne " murmushi yayi ya kwantar da ita a jikinsa yana bubbuga bayanta" toh me abun kuka a ciki..keda xakiyi murna Allah ya amsa mana rokon mu" "Abba Nah is only 6months old fah" "don't worry my pretty ki kwantar da hankalin ki ok..Allah ne ke rayawa notin will hpn to him am sure" haka ya cigaba da kwantar mata da hankali tare da dadadan kalamai.babu yanda ta iya dole ta cire Abba a nono saboda xai iya masa illah..madara ake basa

mami ta samu wata dattijuwa tana kula dashi yanda ya kamata , Ruhaimat na matukar jin tausayin yaron Amma shiko bai damu bah dama can bashi da rigima.wata 2 tayi a Abuja sannan suka shirya suka je yola daga nan ta wuce jada tare da Mimi da kuma nannyn Abba babah larai dattijuwar arxiki, kwanci tashi ckn Ruhaimat ya kai wata 9 da kwana 14 ta sankato danta fari Sol mai kama da ubansa sak! A jada ta dawo ta haihu a wannan karon ranar suna yaro yaci sunan baban sadeeq.batayi wani taron azo a gani bah saboda wani dalili kamar haka ( * wata mata ta haihu a wani gari ..anyi taron suna ta samu kaya masu dumbin yawa bayan suna da sati 1 Allah ya mata rasuwa, aka je binneta abun yaci tura idan aka kwantar da ita sai kasa ya jefata waje..anyi hakan yakai sau 3 sai aka nemo wani malami yaxo yace matar aure ce? Aka amsa mishi nan ya nemi ganin mijin ya tambayesa "shin ko akwai laifin da matarka take aikatawa Wanda ya sabawa Allah? Mijin yace aa..ta kasance mace mai yawan ibada tana matukar kyautata min", a takaice dai mijin matar nan ya bada kyakkyawar shaida akanta haka nan iyayenta sun yaba da halayenta..sai malamin yace "shin akwai Wanda yake Binta bashi? Aka ce "a'ah daga karshe dai basu gano laifinta bah,malamin ya tamabaya ko rashin Ify tayi nan aka sanar dashi ta haihu har anyi suna angama Ify..malam yace "wannan kayan sunan su suka hanata kwanciyar kabari" jama'a suna mamaki , malam ya cigaba da cewa "wasu matan suna bayar da kaya ne tamkar bashi suna sa ran cewa idan sun haihu xaa biyasu ko fiye da Wanda suka kai..donhaka a maidawa kowacce kayan da ta kawo a bar na iyayenta da kuma na mijinta, saboda wannan kayan tamkar bashine a gareta idan bata biya bah xata hadu da axaba..bishara ce Allah ya nuna musu" hakan kuwa akayi aka maidowa kowacce kayanta wasu sun karba wasu ko sunce sun yafe daga nan aka binne matar ba tare da fuskantar matsala bah .. *true life story*..Allah yasa mugane..wllhi daya wa mata basa yin Abu don Allah suna yi ne don idon jama'a ko don a maida musu makamancin Wanda suka bayar ko fiye da haka.hakan ya taba faruwa a unguwar mu inda wata mata ta kaiwa makociyarta turmin xani, ita kuwa makociyar ta kai mata zani 2 nan aka fara kananan maganganu..Allah yasa mu dace ..amin )
Ruhaimat bata gayyaci jama'a bah duk Wanda yaxo don kansa shikenan, haka suka gama taro Ify bayan ta gama wanka ta shirya ta  koma Abuja don sadeeq ya koma can da aikinsa imran da Ibrahim su suke kula da *amz* na yola.

*Reefat ce*😘😘😘😘

💞💞 *MAI SONA*💞💞
*75*
By *Reefat yahya*

*an imaginary Lov story*
🔚🔚🔚

_Alhamdulillah..godiya ta tabbata ga Allah ( s.w.t ) da ya bani ikon kammala wannan labarin Allah yasa mu dace amin_ *godiya gareku masoyana Allah yabar mu tare Lov u all*😘😘😘

Ruhaimat ta koma Abuja Ify haka suka cigaba da rayuwarsu ckn jin dadi da kwanciyar hankali suna matukar nuna wa juna so, basu rabuwa sai idan sadeeq ya tafi wajen aiki kullum suna

makale da juna ga yaransu gwanin sha'awa Mimi an girma tana matukar kama da baba karami tamkar an tsaga kara.

****Xaune suke a falon mami gaba dayansu Mimi Ya'r shekara 7 ta juya gun mami tace "mami nafi Abba kyau koh" dariya suke Ruhaimat ta juya tana kallon Abban nata Dan shekara 2 tace "don't mind her Abba Nah..duk gidan nan ka fisu kyau" murmushn jin dadi yake dama basa shiri da Mimi ko kadan suna matukar kishin juna , sadeeq yace "mmi Nah tafi kyau don tana kama da ni" Mimi tayi carab tace "yawwa dad Shiyasa aka ce kuma kama da little baba koh" kai ya gyada mata cike da jin dadi ta juya tana yiwa Abba gwalo nan ya fashe da kuka sadeeq ya jawosa "sorry sadeeq Dan sadeeq jikan sadeeq kafi kowa kyau duk duniya babu Wanda yafi ka kyau ok" haka ya fara rarrashinsa mami tace "oh..shi wannan babu inda yabar mahaifiyarsa wato har wannan shagwaba saida ya dauka" dariya Ruhaimat take dai2* nan baba ya shigo tare da sallama yaran suka ruga suna masa oyoyo nan ya xauna aka cigaba da hira.da safe sadeeq yace Ruhaimat ta shirya xata raka shi unguwa nan ta dauki dogon hijabinta ta sanya daga nan suka fita sun bar yaran gun babah larai , tafiya mai nisa sukayi sannan yayi parking dai2* wani kayataccen gini aka wangale gate suka shiga ciki ..wow..masha Allah filin ya hadu wani katafaren story building mai kyawun gaske ya bude mota ya fito ya xagaya bangaren ta ya bude mata.tsayawa tayi tana kallon building din yafi amz company haduwa wajen shiru alamar babu mutane a ciki sai masu gadi "ina ne nan kismat?" Murmushi yayi tare da cewa "cloz ur eyes" haka ta rufe idanunta ya rike mata hannu sunyi tafiya kadan yace ta bude ido tana bude wa taci karo da rubutu ckn manyan harufa *AA JADA COLLEGE OF ISLAMIC STUDIES N RESEARCH CENTRE* ta juya tana kallonsa murmushi ya sakar mata tare da rike hannunta yana wasa dashi yace " Ruhaimat kin bani komai na rayuwa kina sona fiye da yanda kike son kanki ..kina bani kulawa ta musamman..kina kyautatawa iyayena da yan uwana kina matukar girmamasu..kina sona ba don wani Abu nawa bah..baki taba bude baki ki rokeni wani Abu bah duk da nasan kina bukata...kin bani dukkan farin ciki na Rayuwa don haka na Gina miki wannan makarantar na mallaka miki shi har abada ko bayan raina wannan baya ckn gado tnx for evrytin I Lov u so much" hawaye ne ke xuba a fuskarta bata da bakin da xatayi amfani dashi wajen yin godiya don haka ta fada jikinsa ta dinga rusa kuka dakyar ya rarrasheta daga nan yabi ya nuna mata koina ckn fadin makarantar abun ba'a cewa komai don karshen tsaruwa kam ya tsaru.bayan sun koma gida ta sanar da mami da baba ta kara musu godiya daga nan ta fara bugawa yan uwanta waya tana shaida musu, a wanna ranar sadeeq ya samu kyauta ta musamman ..hmmm abar kaza ckn gashinta.bayan sati 2 anfara bada admission a makarantar ckn kankanin lokaci yaran masu hannu da shuni suka cika makarantar a yayinda ta bada admission 200 kyauta ga marayu , manyan malamai masu ilimi aka dauko daga kasace daban2* masana addinin islama har da yan kasar mu Nigeria nan aka sa ranar bude makarantar. Yan uwa da abokan arxiki babu Wanda baizo bah ranar bikin bude makarantar, Abba umma Hajja Dada yasmeen imran Ibrahim momin imran da dadynsa da iyayen yasmeen meenah Ameena ya Yusuf anty maryam anty Xee da sauran yan uwa da kuma danginsu na kano duk sun halarta,manyan kusocin gwamnati da manyan yan kasuwa dakuma talakawan gari duk sun hallara a wajen nan Ruhaimat ta fara gabatarwa da harshen larabci daga bisani tayi da turanci tunda ta fara magana ake jinjina mata har ta gama..haka dai aka cigaba da gudanar da programs daga karshe aka tashi da adua.bayan sun koma gida bakin na masauki Ruhaimat na xaune ckn yan uwanta ta chaba ado tayi kyau sosai anty maryam ta tabe baki tace

"oh duniya..Ruhaimat da nake rainawa nake mata kallon bagidajiya Yau ita ta xame mana abar alfahari a duk fadin danginmu" yasmeen tace "hmm kedai bari kawai ni xan baki wannan labarin" anty Xee ta kyalkyale da dariya tace "abunda ka shuka shi xaka girba..hijabin nan dai da kuke raina wa Yau shiya saye mata girma da daukaka a idon duniya" karar wayar Ruhaimat ne ya katse musu hirar daga nan ta tashi tace " *mai sona* yana son ganina na barku Ify" "mu bamu sonki kenan" meenah ta fada ckn xolaya dariya tayi ta fice daga dakin. Kwance yake bisa darduma hannu ya mika mata nan ya jawota ta fada saman kirjinsa " I miss u so much maini" "miss u more mai sona" "my Dil ( xuciya) my pretty i Lov u" "mai sona my kismat my sadeeq my Bbn sadeeq ina matukar kaunar ka Allah yabarmu tare har abada har a gidan aljanna Allah yasa Kaine mijina" "ameen maini..I Lov u more Dan anything in dis world" "Lov u more *mai sona*"
*TAMMAT BIHAMDILLAH* _anan na kawo karshen labarin mai sona abubuwan da na rubuta bisa kuskure Allah ya yafe min , wannan labarin kirkirarre ne banyi shi don cin zarafin wani ko wata bah Allah ya ganar damu yasa mu dace ameen Lov u all_😍😍😍
*littafan Reefat yahya*
~shine zabina~
~nida shugaban kasa~
~mai sona~

*Gareku masoyana*
_Gidan gyara_
_professional writers_
_manshart novel_
_duniya novels_
_xahra bukar novels_
_home of novels_
_matan arewa_
_manyan mata novels_
_Hausa novels_ da sauran groups da ban lissafa bah..Lov u all😘😘

*cutee* *manshart( kishias)😜😜 Nah* *mjay Nah* *billy s fari* *miss xoxo* *hafsy rano* *little princess* *daso ( miemie b)* *billy Ibrahim* n masoyiyata *laurex😜 ( billy losh)* *ayusha iliya* *rabia SK* *Xee yabour* *badiat ib* Lov all

_maman haisam_
_maman afra_
_hasmad_
_only bro Auwal_
N my _fine fine bobo haneef_ Lov u wujiga wujiga
😍😍😍

💞💞💞💞💞💞💞